RAHA A WASU WAQOQIN ALIYU NAMANGI

NA

GARBA LAWAL
MA/ARTS/00163/2008-2009

A Thesis Submitted to the School of Post Graduate Studies, Ahmadu Bello University, Zaria. In partial fulfillment to the requirements for the Award of Degree of Master of Arts in African Languages (Hausa). Department of African Languages and Cultures, Ahmadu Bello University, Zaria-Nigeria.

May, 2014

Declaration

I hereby declare that the work in this thesis titled Raha A Wasu Waqoqin Aliyu Namangi "Comedy in Some of Aliyu Namangi's Poems" was prepared by me in the Department of African Languages and Culture under the supervision of Dr. B.S.Y. Alhassan and Professor Munnir Mamman.

The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this work has been presented for another Degree or Diploma at any institution.

_____ _____

Garba Lawal Date

Certification

This Thesis titled *Raha A Wasu Waqoqin Aliyu Namangi* "Comedy in Some of Aliyu Namangi's Poems" meets the regulations governing the award of Degree of Masters in African Languages of Ahmadu Bello University, Zaria and approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

_____	_____
Dr. B.S.Y Alhassan Chairman, Supervisory Committee	Date
_____	_____
Professor Munir Mamman Member Supervisory Committee	Date
_____	_____
Dr. Balarabe Abdullahi Head of Department	Date
_____	_____
Professor Adebayo A. Joshua Dean, School of Postgraduate Studies	Date

Dedication

This Thesis is dedicated to the memory of my late father Alhaji Lawal Umar Gwangwazo and my late mother Hajiya Harira Salihu (Baba). May their gentle souls rest in perfect peace and may they be rewarded with the most exalted heavens, amin.

Godiya

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah maxaukakin Sarki mai rahama da jinqai da ya halicce mu ya kuma ba mu rai da lafiya har na kai ga matsayin kammala wannan xan qwarya-qwaryar bincike, sa'annan kuma ya sauqaqe hanyar kai wa ga biyan duk buqatun wannan bincike da na gudanar. Tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta Annabi Muhammad (S.A.W) da Alayensa da Sahabbansa da dukan waxanda suka bi shi da kyautatawa har zuwa ranar qiyama, amin.

Bayan haka, ya zama wajibi in miqa godiya ta musamman ga jagoran duba wannan aiki, Dakta B.S.Y Alhassan da jagora na biyu Farfesa Munnir Mamman. Domin qarfafa mani gwiwa da taimakon da suka ba ni ta fannonin shawarwari da xawainiyar gyare-gyaren wannan aiki, duk kuwa da hidimomin da ke gabansu suka iya tsayawa domin bayar da gudummuwa wajen samun nasarar kammaluwar wannan bincike. Saboda haka, addu'ata a gare su ita ce Ubangiji Allah (SWT) ya yi musu sakamako da gidan Aljanna, domin yadda suka yi ta xawainiya da ni a kan wannan aiki mai matuqar tarihi a rayuwata da ta dangina.

Haka kuma godiya mai yawa ga Dakta Magaji Tsoho Yakawada, wanda ya jagoranci zaman farko da na biyu, domin ganin wannan aiki ya kai ga nasara, Allah Ubangiji ya biya buqata Duniya da Lahira, amin.

Har wa yau, ina miqa godiya ta musamman ga Dr. Salisu Garba kargi, jami'in kula da harkokin manyan xalibai na wannan Sashe saboda irin xawainiyar da ya yi wajen ganin wannan bincike ya kammala. Saboda haka babu abin da zan ce, sai dai Ubangiji Allah (SWT) ya yi sakamako da gidan Aljanna.

Haka kuma, ina godiya ga Dr. Balarabe Abdullahi, Shugaban wannan Sashe na Harsuna da Al'adun Afirka, don irin tsayin dakar da ya yi wajen ganin wannan aiki ya inganta. Allah (SWT) ya saka masa da alherinsa, amin.

Ba zan gushe ba, sai na miqa godiya ta musamman ga malamaina, saboda yawan fatan alheri da kuma shawarwari da suka bayar, malaman kuwa sun haxa da Farfesa Xalhatu Muhammad da Mal. Adamu Ibrahim Malumfashi da Dakta Haruna Aminu da Mal. Abubakar Muhammad Sarki, da Mal. Sani Usman, da Malam Abdulmumini Shu'aibu da Dakta Aliyu Muhammad Busa da Malama Hauwa Muhammad Bugaje da Malama Halima K. Daura da Dakta Haruna Aminu da fatan Allah ya saka musu da alheri, amin.

Haka kuma Dakta Abdullahi Garba Wurma da Malama Rabi Garba da Malam Muhammad Rabi'u zarruq ina addu'ar Allah Ubangiji ya ji qansu da rahama, ya kuma gafarta musu dukan zunubansu, amin.

Tsakure

Wannan bincike mai taken Raha a wasu Waqoqin Aliyu Namangi. Ya nazarci wasu waqoqin ne daga cikin waqoqin Aliyu Namangi waxanda ake hasashen cewa qunshe suke da zantuttuka na raha a cikinsu. Wannan bincike ya nuna cewa zantuttuka na raha na da matuqar muhimmanci a rayuwar al'umma musamman ma ga al'ummar Hausawa. Haka kuma binciken ya fahimci cewa wannan salo na yin amfani da zantuttukan raha a waqoqin Hausa kan haifar da nishaxuwa, da gundura yayin karantawa ko sauraron waqoqin. Sakamakon haka sai aka karkasa aikin zuwa babi-babi har guda biyar kamar haka: Babi na xaya ya kasance shimfixa ce da ke haskaka aikin baki xayansa. Babi na biyu kuwa ya waiwayi wasu ayyuka ne da suka gabata masu alaqa da wannan aikin. Babi na uku ya bayyana ire-iren hanyoyin da aka bi ne wajen tattaro bayanan da suka taimaka wajen gudanar da wannan binciken. A babi na huxu kuwa an bayyana wuraren da Aliyu Namangi ya sarrafa raha ce a wasu waqoqinsa. Wato kamar waqar Basukur da waqar zambon qazama da waqar Kuntugin Shaixan da waqar Tambihul Anami. Sai babi na biyar a inda aka naxe aikin gaba xayansa tare da bayar da wasu 'yan shawarwari ga 'yan uwa xalibai da kuma manazarta waqoqin Hausa.

Abstract

This research work titled "Raha a wasu waqoqin Aliyu Namangi" (Comedy in some of Aliyu Namangi's poems) comprises of explanations of how the Artist used comedic expressions in some of his poems. The work also made some criticisms on the kinds of comedic statements he used in the poems to entertain the people. At the end of the study, it was discovered that Aliyu Namangi used these statements in his poems in order to strenghten the relationship that exists between him and his relatives even though the poems were spiritual in nature.

QUMSHIYA

Declaration - - - - - - - - ii

Certification - - - - - - - - - iii

Dedication - - - - - - - - - iv

Godiya- - - - - - - - - - v

Tsakure - - - - - - - - - vii

Abstract - - - - - - - - - viii

Qumshiya - - - - - - - - - ix

BABI NA XAYA

SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa - - - - - - - - 1

1.1 Taqaitaccen Tarihin Aliyu Namangi - - - - - 1

1.1.1 Karance-Karancensa - - - - - - - 2

1.1.2 Aikace-Aikacensa - - - - - - - 4

1.2 Dalilan Bincike - - - - - - - 9

1.3 Manufar Bincike - - - - - - - 10

1.4 Muhimmancin Bincike - - - - - - 10

1.5 Hasashen Bincike - - - - - - - 11

1.6 Iyakacin Bincike - - - - - - - 14

1.7 Naxewa - - - - - - - - 12

BABI NA BIYU: WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa - - - - - - - - 13

2.1 Ma’anar Raha - - - - - - - - 13

2.2 Ire-Iren Raha - - - - - - - - 14

2.3 Raha a Rayuwar Bahaushe - - - - - - 16

2.3.1 Raha a Adabin Bakan Bahaushe - - - - - 17

2.3.2 Raha a Rubutaccen Adabin Bahaushe - - - - 24

2.3.2.1 Raha a Qagaggun Labarai na Hausa - - - - - 25

2.3.2.2 Raha a Rubutattun Wasannin Kwaikwayo na Hausa - - - 27

2.3.2.3 Raha a Rubutattun Waqoqin Hausa - - - - - 29

2.4 Ayyukan Da Suka Gudana Kan Aliyu Namangi - - - - 30

2.4.1 Kundaye - - - - - - - - - 30
2.4.2 Littattafai - - - - - - - - 34
2.4.3 Muqalu - - - - - - - - - 36
2.5 Ayyukan da suka Gudana kan Raha - - - - - 38
2.5.1 Kundaye - - - - - - - - - 38
2.5.2 Littattafai - - - - - - - - 42
2.6 Ayyukan da Suka Gudana Kan Rubutattun Waqoqin Hausa - - 43
2.7.1 Kundaye - - - - - - - - 43
2.7.2 Littattafai - - - - - - - - 48
2.7.3 Muqalu - - - - - - - - - 53
2.8 Naxewa - - - - - - - - 59

BABI NA UKU

HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

3.0 Gabatarwa - - - - - - - - 60
3.1 Xakunan Karatu - - - - - - - 60
3.2 Ziyara - - - - - - - - - 61
3.3 Ganawa/Hira da Wasu Mutane- - - - - - 61
3.3.1 Hira da Malam Umar - - - - - - - 62
3.3.2 Hira Da Murtala Namangi - - - - - - 63
3.4 Ra'in Bincike - - - - - - - - 64
3.5 Kammalawa - - - - - - - - 65

BABI NA HUXU

RAHA A WASU WAQOQIN ALIYU NAMANGI

4.0 Gabatarwa - - - - - - - - 66
4.1 Raha Barkwai a Wasu waqoqin Aliyu Namangi - - - 66
4.2 Raha Faxi-in-faxa a wasu Waqoqin Aliyu Namangi - - - 76
4.3 Raha Shaguvau a Wasu Waqoqin Aliyu Namangi - - - 80
4.3.1 Raha Shaguvau Mai Sigar Wa'azi a Wasu Waqoqin Aliyu Namangi 84
4.4 Kammalawa - - - - - - - - 89

BABI NA BIYAR: KAMMALAWA

NAXEWA

5.0 Gabatarwa - - - - - - - - - 90

5.1 Kammalawa - - - - - - - - - 90

5.2 Shawarwari - - - - - - - - - 91

5.3 Naxewa - - - - - - - - - 92

Manazarta

Ratayen Wasu Waqoqin Aliyu Namangi

BABI NA XAYA
SHIMFIXA

1.0 Gabatarwa

Marubuta waqoqin Hausa wasu mutane ne da Allah (S.W.T) ya ba su wata baiwa da hikima da fasaha ga kuma basira wajen shirya waqoqin Hausa a rubuce, domin isar da wasu saqonni masu muhimmanci ga al'umma. Haka kuma sukan shirya waqa su kuma tsara ta a kan abubuwa daban-daban waxanda suka shafi rayuwar jama'a.

Har wa yau kuma kusan kowanne marubuci da irin hanya ko salon da yakan bi wajen tsara waqarsa, duk da cewa mafiya yawa daga marubuta waqoqin Hausa sukan rubuta waqoqinsu ne bisa jigon wa'azi da gargaxi da tarbiyya ko faxakarwa.

Haka kuma wani lokaci marubuta waqoqin Hausa kan yi amfani da wasu zavavvun kalmomi ko wasu zantuka na musamman a waqoqinsu domin samar da raha ko sanya nishaxi a zukatan jama'a saboda hakan zai haifar da rashin gundura ga mai karatu ko sauraron waqoqin Aliyu Namangi.

Aliyu Namangi na xaya daga cikin ire-iren waxannan marubuta waqoqin Hausa wanda ya yi amfani da wasu zavavvun zantuka na raha a wasu waqoqinsa, a inda wannan bincike zai gudana a kansu domin gano ire-iren rahar da ya yi amfani da su a waxannan waqoqin nasa da ake hasashen cewa suna qunshe da zantuka na raha a cikinsu.

1.1 Taqaitaccen Tarihin Aliyu Namangi

Fagen nazari na tarihin rayuwa da ayyukan marubuta waqoqin Hausa, fage ne mai faxi wanda masana da manazarta suka jima suna binciko tarihin xaixaikun

marubuta waqoqin Hausa da ayyukansu, domin bayar da gudummuwa tare da bunqasa wannan fage na adabin rubutacciyar waqa.

Masana da manazarta da dama sun kawo tarihin Aliyu Namangi a aikace-aikacensu da suka gudanar, ire-iren waxannan ayyuka na manazarta kan Aliyu Namangi sun haxa da Skinner (1969) da Xangambo (1973) da Hassan (1973) da Birniwa (1989) da Yakawada (1987) da Sankalawa (2005) da Muhammad (2010) da Muhammad (2011) da Nazifi (2011). Dukkansu sun bayyana cewa an haifi Aliyu Namangi ne a wani qauye mai suna Mangi a kusa da birnin Zariya. Hijira na da shekara dubu xaya da xari uku da goma sha biyar (1315) A.H. wacce ta yi dai-dai da shekara ta dubu xaya da xari takwas da casa'in da huxu (1894) A.D. A ranar Larabgana wato Larabar qarshen watan safar, wato watan biyu na Musulunci.

An kuma haife shi ne a lokacin sarkin Zazzau Kwasau, sunan mahaifinsa Ishaq, sunan mahaifiyarsa kuwa Hauwa'u. An haifi Aliyu Namangi lafiyarsa qalau kamar sauran jarirai. Bayan shekara xaya da haihuwarsa a watan safar sai idanunsa suka tsiyaye a sakamakon rubdugun cutar 'qyanda' da ta 'Agana' da suka same shi a lokaci xaya. Wannan shi ne musabbabin makancewar Aliyu Namangi, kuma an yi masa kaciya yana da shekara bakwai da haihuwa. (Yakawada, 1987:6-8).

1.1.1 Karance-Karancensa

Bayan an yi wa Aliyu Namangi kaciya ya warke sai mahaifinsa ya danqa shi a hannun wani malami mai suna malam Ibrahim domin ya karantar da shi Alqur'ani mai girma. Fara karatunsa ke da wuya sai malam Ibrahim ya yi qaura

daga garin Mangi, sai aka mayar da shi wurin malam Gambo, a wurinsa ne, ya yi karatun Alqur'ani har zuwa izu huxu. A lokacin da malam Gambo ya tashi yin qaura daga garin Mangi zuwa cikin birnin Zariya bai bar Aliyu Namangi a baya ba, tare suka tafi (Muhammad 2010: 57-58).

Bayan da Aliyu Namangi ya kai shekara goma sha shida da haihuwa sai mahaifinsa ya yi masa kyautar wata baiwa. Da ya kai shekara ashirin da xaya, sai mahaifinsa ya yi masa auren fari. Duk da larurar ido da kuma auren da aka yi masa, bai hana shi neman ilimi ba. Ba kamar sauran xalibai masu gani ba Aliyu Namangi haddace karatunsa kullum yake yi sai ya kawo haddarsa kafin a xora masa wani sabon karatun. Duk da cewa ba ya gani shi ma ana rubuta masa ne a allo kamar sauran xalibai. Idan ya mance da karatunsa, sai qaninsa Abdulqadir ya tuna masa, idan ya duba allonsa. (Muhammad (2011:30-32)

Aliyu Namangi bai tsaya a kan karatun Alqur'ani kaxai ba, ya yi karatun wasu fannoni na ilimi a wajen malamai da dama. Daga cikin littattafan da ya karanta akwai Qawa'idi da Ahlari da Ishimawi da Iziyya da Risala da Askari da muhutasar da tafsiri da sauran littattafan addini.

Neman ilimin Aliyu Namangi ba wai kawai a Mangi ya tsaya ba ya yi tafiye-tafiye da dama domin neman ilimi wurin malamai daban-daban kamar irin su malam Muhammadu Gwandu da malam Na'iya Zariya, da malam Ramalan Limamin Wushishi, da malam Yahuza Zariya, da Malam Sa'idu Kusfa Zariya, da malam Na'ta'ala Wusono, da malam Abdulqadir Banufe, da dai sauransu.

Bayan waxannan malaman waxanda suka taka rawa a rayuwar Aliyu Namangi ta fannin ilimi, sai Shitawa (zuriyar Shitu xan Abdurra'uf). Domin shi

da kansa ga abin da yake cewa a waxannan baitoci na waqarsa ta "*Imfiraji*" juzu'i na biyu.

Ni da Shitawa na saba,
Tun gaban ban hankali ba,
Sun riqe ni, riqon da ba,
Duka xa a kai ma shi ba,
Im ba gatansa tai yawa ba.

Shaihuna Abdurra'ufi,
Tun ina yaro la'ifi,
Ya riqe ni riqon nazifi,
Har ya zam na fara qarfi,
Bai bar ni cikin hakukuwa ba.

Shi ya ce min "kai karantu",
Ko da ba ka gane ka wadatu,
Dubi Tahamisin Tafattu"
Sai ban ji rabo kamar sani ba.

(Yakawada, 1987:7-8)

1.1.2 Aikace-Aikacensa

Duk da cewa Aliyu Namangi ya karanci littattafai na addini da na waqoqi kamar su Alburda wacce Busari ya rubuta, da *Ishiriniyar* da *Alfazazi* ya rubuta da dai sauran littattafai na waqoqi waxanda ba Aliyu Namangi kawai suka qarfafa wa gwiwar wallafa waqoqi ba, har ma da sauran tsofaffin marubuta waqoqi musamman ma masu jihadi. Waxannan littattafai da waqoqin *Madahu* sun burge Aliyu Namangi. Amma kuma bai tava tunanin rubuta waqa ba, sai da ya ji waqar "*Jiddul Ajizi*" Ba'ajamiya, ta malam Shitu Xan Abdurra'uf daga bakin abokin bararsa mai suna malam Lawal Xan Limamin Jaji malam Adamu. Shi malam Lawal ba makaho ba ne, amma saboda almajiranci yake bara da Aliyu Namangi. Daga nan sai ya roqi Allah da ya ba shi fasahar iya tsara waqa, wacce ta yi kama da ta malam Shitu xan Abdurra'uf. Bayan da Allah maxaukakin Sarki ya hore wa Aliyu Namangi fasahar iya tsara waqa, sai ya fara rubuta tasa waqa wacce ya raxa

mata suna *Kanzil Azimi* (Babbar Taska) wannan waqa tana da baiti dubu biyu, amma waxanda aka iya samu a yanzu su ne dubu xaya da xari shida da hamsin da biyu (1652). Kuma ita ce waqarsa ta farko. Har wayau, ta qunshi jigon wa'azi da madahu. A sashen wa'azi kashin waqar na farko yana cewa:

(55) Mu san Ta'ala xai na mu tabbatu,
Sarki ne da buwaya da girmansa Jalla mai iko.

(56) Komai yai hani da shi ba ta kansa ke nan,
Mu tsarci abin da yai hani, in muka bar shi ma ga alhairi.

A kuma sashen waqar kashi na biyu, wato na yabon Annabi (SAW) sai ya ce:

(1110) Allah ka buxe basiran sani garan
In yabi Annabinka Sidi Muhamman bisa hali goma

(1111) Lizimci wannan suna da ambato
Ko washe kai nufin yabo nasa lada dubu ake ba ka,

(1112)Yabo Sayyidil munji ko a ko'ana
Kowashe ka faxo ma'aikin Allah ba ka yi savo ba.

Daga nan kuma ya qara yin wata waqar wacce ita ce waqarsa ta biyu, ya yi ne domin yabon Annabi (S.A.W) mai suna "Tarjimul Shariri" (wato jifan shaixan). A inda yake cewa:

Bismillahi zan fara da waqa,
Arrahmani Summar Rahimi,

Mai kotso da Baraga da Jauje,
Kowa na yabon hakimainai.

Ni da na xinka gangar yabona,
Sai na nufe ka Hairal bariya,

Annabi ya fi sauran halitta,
Ba fikon savi ko taqa ba.
(Yakawada, 1987:8-9)

Kamar yadda aka gani, waqoqin da aka ba da misali da su duk ba su da amsa-amo, amma waqarsa ta uku ita ce waqa ta farko da ya fara yi wa amsa-amo.

Wannan waqa kuwa ita ce, waqar '*Imfiraji*' ya yi wannan waqa ce sakamakon roqon da aka yi masa da ya shirya waqar da muryar waqar caji', ta yabon Manzon Allah (S.A.W.) wacce ta yi wannan roqon ita ce 'yarsa ta fari mai suna Hauwa, wacce take auren Limamin Gargai a wancan lokacin. A bisa al'adar Bahaushe akwai kunya tsakanin xan fari da mahaifansa. A sakamakon haka, sai ta shaida wa kishiyarta mai suna Ajuji. Da jin haka, sai Ajuji ta tafi ta shaida wa Aliyu Namangi buqatar da Hauwa take da shi. Da ya tashi biya wa 'yarsa wannan buqata tata, sai ya yi kara irin ta mutanen da, bai ambaci sunan 'yarsa ba a matsayin wacce take da buqatar, sai ya ambaci sunan kishiyarta Ajuji wacce aka aika. Hakan ya tabbata a cikin waqar a baiti na 67 inda yake cewa:

Wanga talifi da na ji,
Waqe-waqen masu caji,
Nai ma 'yata ce Ajuji,
Sai na sa mata Imfiraji,
Mai yin ta ba zai baqin ciki ba.

(Yakawada, 1987:9-10)

Waqar da ke bi wa '*Imfiraji*' ita ce waqar "*Katifa*" wacce ya samo karinta daga wasu Bare-bari da suka zo Zariya suna yin wata "waqar Kwambilo" ya yi wannan waqar ce saboda buqatar da matarsa ta yi masa da ya yi waqar. Ga yadda ya fara waqar *Katifa*

Allah, Ta'ala ka ban
Waqar da ta zan daban
Da tasu, domin yabon
Maxaukaki, shugaban
Duka, sayyadil Ambiya.

Ya Arrahmar Rahimi,
Na, qara so da'imi
Ga musxafal ka'imi,

Muhammadu Hashimi,
Mai magani don wuya
(Yakawada, 1987:9-10)

Haka kuma ya yi wata waqa mai suna ‘waqar ‘Nafisa’, ta yabon Annabi (S.A.W) ya kuma faxi sunan waqar a baitin qarshe inda yake cewa:

Ga waqa Nafisa,
Nakan ji Lawal da Isa,
Sukan ta wajen Wusasa
A ce Gude na da Hausa,
Da sai ta iya ta tsira.
(Yakawada, 1987:10-11)

Daga nan kuma sai ya wallafa “waqar *Basukur*” a shekarar (1959) ya yi wannan waqa ta “*Basukur*” ce, a lokacin bukin samun mulkin kan Arewa. A wannan lokaci ne aka buqaci mawaqan baka da marubuta da su shirya waqoqi, don murnar bukin. An ba su damar yin waqar da suke so dangane da zuwan Turawa qasar Hausa da samun mulkin kai saboda haka sai Aliyu Namangi ya tsara wannan waqa ta “*Basukur*”, inda yake cewa:

Muna shukura ga Rabbal Alamina
Da Alherin da yai mana ba kaxan ba,

Muna murna da mulkin Ingilishi
Zuwad da suka yi qasarmu ba tai tsiya ba.

Zama zamaninsu ne aka zo da faifa,
Kuxi ba masu nauyaya aljihu ba.
(Yakawada, 1987:11-13)

Baya ga waqar *Basukur*, sai waqar *Kuntigin shaixan*. Ita wannan waqa an yi ta ne da nufin yi wa jama’a gargaxi, da su bar aikata laifi suna cewa shaixan ne ya yaudare su, domin kuwa ranar lahira shaixan zai qaryata zargin da suke masa, kuma ya kaxa molonsa yana yi wa ‘yan wuta dariya yana cewa:

Aha yayyayye aha iya,
Ursatu ku bar zargi na,

Da an muku doka kun qi ji,
Ku kai aiki mummuna

Aka sa ku ibada kun qiya
Halinku ya zam tamkana

Ana sallah da subahi
ku yi naku da rana.
(Yakawada, 1987:13-14)

Daga wannan waqa kuma sai waqar *Qazama,* domin wa'azi ga jama'a game da auren mata *Qazama*i da su kansu mata *Qazama*i da su daina qazanta, inda yake cewa:

Ya Allahu, Rabbana, taimake mu,
Mu gargaxi 'yan'uwa da auren Qazama.

Auren tsohuwa hasara ga yaro,
Gwammaci tsohuwa ga auren Qazama.

In ba ka san ta ne ba kau tambaye ni,
In Allah ya yarda ka san Qazama.

Mummunan halin Qazama na fari,
Ba ta fyace majina sai da dama.
(Yakawada, 1987: 14-15)

Baya ga waxannan waqoqi da aka bayyana a baya, Aliyu Namangi ya wallafa wasu waqoqi da dama waxanda ke da jigo dabam-dabam. Waxannan waqoqi sun haxa da:

Waqar Qahon Karo
Waqar Irshadil Qulubi
Waqar Fasalu ma Yadibu fi haqqihi Ta'ala
Waqar Fasalu ma Yastahihu fi haqqihi Ta'ala
Waqar ma Yajibu Shukura fi haqqihi Ta'ala
Waqar Ma Yakunu fi haqqihi Ta'ala

Waqar ma Yajuzu fi haqqihi Ta'ala

Aliyu Namangi ya samu Digirin girmamawa daga Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zariya a fannin rubuce-rubucen waqoqin Hausa a ranar 2 ga watan Disamba shekara ta alif xari tara da saba'in da takwas (1978). A wurin wannan biki ne, ya rera wata waqa mai suna waqar *Murnar Samun Digirin Girmamawa.*

A qarshe Aliyu Namangi ya rasu a ranar 27-4-1994. A lokacin yana da shekara xari da biyu (102). Shekara xari a kalandar Nasara. Amma wajen shekara xari da biyu a kalandar Musulunci.

Aliyu Namangi ya haifi 'ya'ya 64 a Duniya, amma ya rasu ya bar 'ya'ya (21) maza goma sha huxu mata bakwai (7) matan aure guda (4). An haife shi ranar Laraba ya rasu ranar Laraba. Allah ya jiqansa da Rahamarsa, amin. (Yakawada 1987:15-16)

1.2 Dalilin Bincike

Duk da cewa an gudanar da bincike-bincike game da raha wasu kuma dangane da ire-iren gudummuwar da Aliyu Namangi ya bayar wajen havaka rayuwar al'ummar Hausawa ta fuskar addinin Musulunci, ta hanyar wa'azantarwa da faxakarwa a cikin waqa. Sa'annan kuma an san Aliyu Namangi a matsayin malami kuma mai waqoqi kan wa'azi da madahu.

(i) Amma sai ga shi raha na xaya daga cikin salailan da suka yi fice a waqoqinsa, saboda haka wannan bincike zai bincika ya gano hikimarsa ta yin amfani da wannan salo na raha a waqoqinsa.

(ii) Haka kuma an lura da cewa manazarta sun gudanar da aikace-aikace da dama kan raha amma mafiya yawa daga cikinsu sun fi karkata ga qagaggun labarai da tatsuniyoyi da kuma wasannin kwaikwayo na Hausa.

(iii)Wata hujjar kuma ita ce an zavi gudanar da binciken ne a kan wasu waqoqin Aliyu Namangi masu qunshe da zantuka na raha a cikin su. Domin an bincika an ga cewa akwai qarancin bincike game da ire-iren waxannan waqoqi masu qunshe da zantuka na raha.

1.3 Manufar Bincike

Haqiqa babu wani bincike da za a gudanar ba tare da wata manufa ba. Saboda haka, yana daga cikin manufar gudanar da wannan bincike:

(i) Gano hikimar Aliyu Namangi wajen yin amfani da salon raha a waqoqinsa.

(ii) Qara tabbatar da cewa zantuka na raha na da muhimmanci ga al'umma saboda baya ga haifar da nishaxi, wata hanya ce mafi sauqi wajen isar da saqo ga jama'a.

(iii) Bin diddigin hasashen da ake ganin cewa a duk lokacin da aka ji wasu zantuka na raha za a taras da cewa wani abu ne da ya shafi wasa, babu gaskiya a tattare da shi.

(iv) Har wa yau kuma za a yi qoqari a gano shin mece ce hikimar mawallafin ta yin amfani da ire-iren waxannan zantuka na raha a waxannan waqoqi da ya wallafa?

1.4 Muhimmancin Bincike

Waqa muhimmiyar hanya ce ta isar da saqo ga al'umma, kuma hanya ce da za a iya fahimtar tunani da fasahar mutum ga kuma sanya nishaxi a tsakanin al'umma. Saboda haka yana da matuqar muhimmanci a gudanar da wannan

bincike a wasu waqoqin Aliyu Namangi masu qunshe da zantuka na raha a cikin su.

(i) Domin zai qara zaburar da ‘yan’uwa manazarta da su qara zage damtse wajen gudanar da bincike kan nazartar raha a wasu rubutattun waqoqin Hausa da ma na baka.

(ii) Haka kuma binciken yana da muhimmanci domin za a yi qoqarin fito da baitocin da suke qunshe da zantuka na raha daga waqoqin da aka nazarta, sannan kuma a taskance su a matsayin wani aiki na adabin (rubutattun waqoqin Hausa), kuma su zama masu alfanu ga sauran manazarta.

(iii) Har wa yau ana fata wannan bincike ya zamo fitila ga sauran marubuta waqoqin Hausa ta yin amfani da irin wannan salo na zantuka na raha a lokacin da suke rubuta waqoqinsu saboda samar da nishaxi ga masu karatu ko sauraron waqoqin domin gudun gundura da waqoqin.

1.5 Hasashen Bincike

An lura da cewa akwai qarancin bincike game da abubuwan da suka shafi raha a rubutattun waqoqin Hausa. Saboda haka, yana daga cikin hasashen da suka haifar da wannan bincike, wato domin a gano:

(i) Matsayin raha a idon Bahaushe

(ii) Yadda al’ummar Hausawa suke kallon duk mutumin da suke amfani da zantuka na raha a wallafarsa.

(iii) Matsayi ko jigon waxannan waqoqi masu qunshe da zantuka na raha a cikinsu.

1.6 Iyakacin Bincike

Hausawa kan ce komai na da iyaka, amma ban da ikon Allah, domin haka ya zama wajibi ga duk wani mai gudanar da bincike a kan wani batu a san iyakar da'irar ko farfajiyar da bincikensa zai gudana.

Manazarta kan yi hakan ne, domin kauce wa cin karo da wani aiki da ya yi daidai ko kama da nasu domin gudun kar a maimaita aikin da wani ya gudanar.

Hakan zai samar da aiki ingantacce kuma karvavve wanda jama'a za su amfana da wasu abubuwan da ba su san da su ba. Saboda haka, an taqaita wannan bincike ne a kan wasu waqoqin Aliyu Namangi da ake hasashen cewa suna qunshe da zantuka na raha a cikin su.

Waqoqin kuwa su ne (i) waqar *Basukur* (ii) waqar *Zambon Qazama* (iii) waqar *Kuntigin Shaixan* (iv) waqar *Tambihu Anami* (faxakar da jama'a).

A taqaice dai waxannan waqoqi guda huxu su ne aiki zai duba domin nazartar ire-iren zantuttukan raha da ke cikin su.

1.7 Naxewa

Tun a farkon wannan babi aka kawo shimfixa wacce ta gabatar da yadda za a gudanar da wannan bincike inda aka yi taqaitaccen bayani kan yadda marubuta waqoqin Hausa ke tsara waqoqinsu, haka kuma an yi bakandamiyar shimfixa da ta shafi kusan dukkan abubuwan da za a duba a lokacin gudanar da wannan bincike.

Bayan nan an kawo dalilan bincike wato abubuwan da suka haddasa gudanar da wannan bincike, sai manufar bincike wato makomar wannan bincike

idan ya kammala, sannan kuma sai aka bayyana muhimmancin binciken wato irin gudummuwar da binciken zai bayar musamman ma a wannan fage na ilimi.

Daga nan kuma sai aka tantance hanyoyin da aka bi wajen gudanar da binciken da iyakar binciken mai nuna inda da'irar binciken za ta tsaya.

BABI NA BIYU:

WAIWAYEN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Gabatarwa

Babu shakka an gudanar da bincike-bincike game da raha a rayuwar al'umma da ire-iren gudummuwar da Aliyu Namangi ya bayar a lokacin rayuwarsa, sai kuma masu magana game da rubutacciyar waqar Hausa.

Saboda haka, ayyukan da za a waiwaya domin yin bita a kan su za su kasance ko dai sun shafi bayani da sharhi kan xaya daga waxannan vangarori, ko kuma dukkansu ta hanyar nuna wuraren da suke da kamanci ko bambanci.

Domin ta haka ne za a san abin da aka tava da wanda ba a tavo ba, hakan zai ba da damar sanin inda alqiblar wannan aiki ta dosa, kuma ma Hausawa kan ce "Waiwaye adon tafiya". Saboda haka, za a nazarci kundayen bincike waxanda

aka gudanar a fannoni daban-daban kuma a jami'o'i daban-daban a matakin digiri na xaya zuwa na uku.

Bayan nan kuma za a nazarci littattafai waxanda masana suka wallafa, sai kuma muqaloli da qasidu masu alaqa da wannan bincike kai tsaye ko a fakaice.

Har wa yau kuma duk a wannan babi ne za a kawo ma'anar raha da ire-iren raha da kuma yadda raha take a rayuwar Bahaushe ta gargajiya da ta zamani, sannan kuma a kawo taqaitaccen tarihin rayuwa da wasu aikace-aikacen Aliyu Namangi.

2.1 Ma'anar Raha

Raha wata aba ce da ke haifar da nishaxi ga al'umma wadda ake aiwatar da ita ta hanyar yin amfani da wasu zantuka na musamman ko kuma a aikace a wasu lokuta na musamman domin nuna farin ciki da annashuwa. Saboda haka a duk lokacin da aka yi magana game da raha ba ya wuce amfani da wasu zantuka ko kwaikwayar murya ko wasu xabi'u ko tsokana a tsakanin mutane musamman ma waxanda akwai wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu.

Manufar dai ita ce a samar da nishaxi ko bayar da dariya ga abokanan zama ko hulxa (Aminu, 2012: 53-54).

Masana da manazarta adabin Hausa da na Turanci sun bayyana ma'anar raha dangane da fahimtarsu. Umar (1981) ya ce "Raha magana ce ta ban dariya" ko a ce "Raha Magana ce ta ba'a da takan faru ga mutum ko a tsakanin mutanen da suka amince akwai wasa a tsakaninsu", ya kuma qara da cewa "Maqasudinta shi ne ta haifar da nishaxi a tsakaninsu".

Shi kuwa Bargery (1993) cewa ya yi “Comedy is a pleasant, chatting, playful teasing” wato (Raha na nufin faxi-in-faxa a cikin wasa).

Yayin da C.N.H.N (2006) suka bayyana raha da “walwala ko fara’a”.

Su kuwa Adebayo (1993) da Wilson & Golfarb (2002) da Stephen (2006) da Abraham & Harpham (2009) sun bayyana raha da “Comedy is that whuich brings about laughter and entertainment to reader or audience”. (wato dukkan wani abu da ka iya sanya mai karatu ko xan kallo dariya).

A taqaice dai bisa ga la’akari da ma’anar da masana suka kawo game da raha wannan ya nuna cewa babban jigo ko manufar raha ita ce haifar da nishaxi da kuma annashuwa.

2.2 Ire-Iren Raha

Masana da manazarta sun kawo ire-iren raha da kuma yadda ake gudanar da kowacce irin raha a tsakanin al’umma.

(i) Raha shaguvau (sataric comedy). Wilson & Golfrab (2002) da Abraham & Harpharm (2009) sun bayyana raha shaguvau da cewa “A comedy performed to ridicule a particular behaviour or foolishness of an individual or a society”.

Abraham (2009) adds that “This kind of performance sataric comedy is done to ridicule a political or philosophical phenomena of a particular society which is presented comecally”. Wato (Akan aiwatar da irin wannan rahar ce, domin sukar wata muguwar xabi’a ko wautar wani mutum ko wata al’umma)

Abrams (2009) ya qara da cewa “Akan aiwatar da irin wannan rahar ce domin kushe wasu dokokin siyasa ko falsafar wata al’umma a kuma gudanar da ita a nishaxance”

(ii) Raha Faxi-in-faxa (chatting comedy). Yahaya (1987) da Umar (1981) da Bargery (1993) sun nuna cewa “Ita irin wannan raha takan samu ne a sakamakon faxi-in-faxa da ke wakana a tsakanin vangarori biyu na mutane”.

Umar (1981) ya qara da cewa “Ba wani abu ba ne raha faxi-in-faxa illa maganganu na ba’a da ke gudana a tsakanin mutum da mutum ko a tsakanin wasu mutane waxanda suka amince da cewa akwai wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu”.

(iii) Raha ‘yan kamanci: Talle (1990) da Aminu (2012) da Zubairu (1992) sun bayyana cewa “Raha ce da masu yin ta kan zaqe a magance ko a aikace wajen qoqarinsu na ratsa raha da nishaxi a zukatan al’umma kamar yadda ‘yan kama kan yi batsa ko su yi tsikari ko wasa da gemu da shaqiyanci da sauransu”.

(iv) Raha kuskurau (Comedy of error). Boulton (1977) da Abram & Herpham (2009) sun bayyana cewa “Comedy of errors often looks and satirizes some mistaken identity of a given people by means of disguising for the purpose of correcting the mistakes that happened”.

Wato (Akan duba wasu xabi’u ne da suka sava wa wata al’ada a sanadiyyar wata ‘yar vatar da kama da akan yi ne domin gyara waxannan kurakurai da suka faru).

(v) Raha Barkwai – Zubairu (1992) da Aminu (2012) sun bayyana raha barkwai da cewa “Raha ce da ake zaqewa wajen qoqarin cusa nishaxi ko ban dariya ga jama’a ko da kuwa za a kai ga faxan wasu munanan zantuka kamar batsa da wasu kalamai da ka iya vata wa wasu rai, wato kamar yadda ‘yan gambara ke yi a waqoqinsu na ban dariya”.

2.3 Raha A Rayuwar Bahaushe

Al’ummar Hausawa na xaya daga cikin al’ummu na duniya da suka gudanar da abubuwa da dama cikin raha domin samar da nishaxi a tsakaninsu. Saboda duk manyan rassa na adabin Bahaushe kusan babu wanda ba a samun ratsin raha a cikinsa domin nishaxi. Kamar irin su waqoqin Hausa da wasannin kwaikwayo da kuma qagaggun labarai, hasali ma dai, idan har ana son wani aikin adabin Bahaushe ya samu karvuwa, sai an haxa da raha a cikinsa.

Saboda haka Hausawa na da hanyoyi daban-daban wajen gudanar da wasu abubuwa cikin raha, domin samar da nishaxi a tsakaninsu, musaman ma, a lokacin da suke cikin farin ciki da annashuwa, dalili kuwa idan aka yi la’akari da waqoqi da tatsuniyoyi da qagaggun labarai da kaxe-kaxe da raye-raye da sauran wasannin motsa jiki waxanda matasa ke gudanarwa da kaka bayan an kai amfanin gona gida. Duk ana aiwatar da su ne cikin raha, domin a samar da nishaxi da annashuwa, kuma lokaci ne, na nuna farin ciki na samun amfanin gona, haka kuma wasannin gaxa da ‘yan mata ke gudanarwa da wasannin langa da dokin dafe da asha ruwan tsintsaye da Allan ba ku da waqoqin tashe, duk ana aiwatar da su ne a cikin raha, bayan an kammala aikace-aikacen gida da na gona.

Daga ire-iren waxannan wasanni ne aka samo vullar waqe-waqe da kaxe-kaxe na raha waxanda ke da sigogin wasannin kwaikwayo irin su ‘yan kama da ‘yan gambara da ‘yan hoto da ‘yan kacakaura da makamantansu

(Xangambo, 1984:13-14).

Saboda haka, ire-iren waxannan zantuka na raha da waqe-waqe na raha, sun samo asali ne daga fadar Sarakunan qasar Hausa sakamakon bayyanar Wawan sarki wanda ke canza kamanni ya rinqa furta wasu zantuka tare da aiwatar da wasu xabi’u da ka iya sanya sarki dariya da samun nishaxi a zuciyarsa musamman ma idan an lura da cewa ransa ya vaci. (Aminu 2012:56-57).

2.3.1 Raha A Adabin Bakan Bahaushe

Haqiqa Hausawa sun gudanar da abubuwa da dama cikin adabinsu na baka waxanda ke qunshe da zantuka na raha daban-daban a cikinsu. Ire-iren waxannan abubuwa sun haxa da tatsuniyar Hausawa wadda yawanci sukan zo ne da labarai na raha ko ban dariya, domin nishaxantarwa. Saboda akan aiwatar da su ne domin yara da nufin koyar da su kyawawan xabi’u amma cikin raha saboda su yaran ba abin da suka fi sha’awa illa abubuwan da za su sanya musu nishaxi da kuma ban dariya duk da cewa ana qoqarin cusa tarbiyya a zukatansu.

Ire-iren waxannan tatsuniyoyi sun haxa da tatsuniyar Gizo da budurwar danqo, wacce Gizo ke yi wa matarsa qoqi wayo ya ce “Ta kawo gyaxa tiya biyu soyayya, domin a shuka”, amma ya cinye. Idan lokacin kawo amfanin gona gida ya yi, sai ya rinqa sato gyaxa a gonar Sarki yana kawo wa gida har dai a qarshe aka yi masa wayo aka kama shi, ta hanyar ajiye budurwa amma ta danqo, a lokacin da yake qoqarin tava budurwar a zatonsa budurwa ce ta gaske. Saboda

haka, yana tava ta ya manne a jikinta, har aka zo aka kama Gizo Sarki ya hukunta shi. Haka kuma a tatsuniyar Idi da gawar bawan sarki wanda aka kashe aka zo xakin Idi aka jingine tamkar wata haja ashe abokinsa ne, ya yi masa haka. A qarshe aka kama shi sarki ya sa aka hukunta shi da horo mai tsanani. A nan babu wani abu mai muhimmanci a waxannan tatsuniyoyi illa, raha da kuma ban dariya. (Aminu 2012:55-56).

Baya ga tatsuniya akwai waqoqin baka da aka gudanar cikin raha domin sanya nishaxi da kuma bayar da dariya ga jama'a. Waxanda aka fi sani da aiwatar da ire-iren waxannan waqoqi na raha domin sanya nishaxi da kuma bayar da dariya su ne 'yan kama da 'yan gambara da kuma 'yan kacakaura. Duk rukunin waxannan mawaqan sukan shafa kwalli ko bula. Sa'annan kuma su sanyan manyan riguna barkatai a lokacin da suke gudanar da waqoqinsu tare da aikata wasu xabi'u da ka iya bayar da dariya ga jama'a kamar rawa da gwalo ko kuka da makamantansu.

Haka kuma sukan gudanar da waqoqinsu ne a ranar kasuwa ko a wajen wani babban taro ko naxin sarauta ko xaurin aure da sauransu. Ire-iren waxannan waqoqi na raha na qunshe da abubuwa da dama kamar kwaikwayon muryoyi ko kukan tsintsaye ko ambaton abinci da nau'o'insa da kirari da addu'a da ba'a da barkwanci da shaqiyanci da batsa da kuka da ihu da sauransu. Su dai manufarsu ita ce su bayar da dariya tare da sanya nishaxi a zukatan jama'ar da ke kallonsu, saboda kwaikwayar muryar da suke yi kamar yadda malam Ashana xan kama ya kwaikwayi karin muryar waqar Duniya ta yi kyau arziqi ya yi ta Mamman Sarkin Taushin Katsina inda yake cewa:

Gindin waqa	: Duniya ta yi kyau arziqi ya yi
	Tun da mun karvi girki ga matanmu
Jagora:	: Kan mun yi girkin da ba mu sanya manja ba,
	:Garas sai nama,
‘Yan Amshi	: Mun yi koyi da girkin qasar London.
Jagora	:Kan mun yi damu da ba mu sa ruwa ba,
‘Yan Amshi	:Sai nono, mun yi koyi da damun qasar Yarwa
Jagora	:Ashe masu tsire da fanke suna yawo,
	:Ga tuwo nan da namansa an qare,
	:Ga fura can da nononta an dama,
	:Masu tsire da fanke suna yawo,
	:Sha biyun rana ka ji ta koka,
	:Mai tubani da xanwake ta qare,
	:Ka saya za ta sa mai ta sa yaji,
	:Ka yi jahilci ka sanya tsinke,
‘Yan Amshi	:In ka yi shan kai ka xiba da hannunka,
	:Duniya ta yi kyau arziqi ya yi,
	: Tun da mun karvi rance mu sha shayi,
Jagora	: Duniya ta yi kyau arziqi ya yi,
‘Yan Amshi	: Na sai cukuna da nono mai mazanqwaila.
Jagora	: In ka ji an ce miya ta yi qauri,
	: Ko ka ji an ce miya ta yi qyalli,
	:An sami manja da kwandon tumatir.

	:Attaruhu dogarai ne a miya,
	:Sai man gyaxa shi ka aikin wakilai,
	:Sai yakuwa ke ta yin farfaganda,
‘Yan Amshi	: Duniya ta yi kyau arziqi ya yi,
	:Tun da mun karvi rance ga matanmu,
Jagora	:In ka ji an ce miya ta yi zaqi.
	:Ko ka ji an ce miya ta yi qyalli,
	:An sami manja da kwandon tumatir,
	:Attaruhu dogarai ne a miya,
	:Sai man gyaxa shi ka aikin wakilai,
	:Ai yakuwa ke ta yin farfaganda.
‘Yan Amshi	: Duniya ta yi kyau arziqi ya yi,
	:Tun da mun karvi rance ga matanmu.
Jagora	: In ka ji an ce miya ta yi zaqi,
	:Ko ka ji an ce miya ta yi qyalli,
	:An sami manja da kwandon tumatir,
	:Attarihu dogarai ne a miya,
	:Sai man gyaxa shi ka aikin wakilai,
	:Ai yakuwa ke ta yin farfaganda.
Y/Amshi	:Duniya ta yi kyau arziqi ya yi,
	:Tun da mun karvi rance ga matanmu.

(Gusau 1993:330-334).

Akwai kuma wannan waqar:

Makaxi: Malam Ashana Xankama.

Jagora : Ahayye yaro,

‘Yan Amshi :Ahayye yaro,

Jagora :Yaranaye kin ji kixa da shana,

‘Yan Amshi : Yaranaye kin ji kixa da shana,

Jagora : Sai malamin ya yarda,

‘Yan Amshi : Sai malamin ya yarda.

Jagora : Yaranaye Allah ya ba ku ku ba mu,

‘Yan Amshi :Yaranaye Allah ya ba ku ku ba mu,

Jagora : Maigida na toshin fire ba goro,

‘Yan Amshi : Maigida na toshin fire ba goro,

Jagora : Ahayye kin latsa mu,

‘Yan Amshi : Ahayye kin latsa mu.

Jagora : Yaranaye wani ya saya ya ba mu,

‘Yan Amshi : Yaranaye wani ya saya ya ba mu.

Jagora : Yaro kawo ruwa kawo ruwa,

‘Yan Amshi : Yaro kawo ruwa kawo ruwa.

Jagora : Yaro kawo ruwa da hanzari,

‘Yan Amshi : Yaro kawo ruwa da hanzari.

Jagora : Yaro matso kusa ka hau gado,

‘Yan Amshi : Yaro matso kusa ka hau gado.

Jagora : Kafin ta farga har ya saya,

‘Yan Amshi : Kafin ta farga har ta saya.

: ya tsere.

Jagora : Ahayye xan shana,

‘Yan Amshi : Ahayye xan shana.

Jagora : Yaranaye kin ji mai kixa xan shana,

‘Yan Amshi : Yaranaye kin ji mai kixa xan shana.

Jagora :Yaranaye wahidun ya ba ku ku ba mu,

‘Yan Amshi : Yaranaye wahidun ya ba ku ku ba mu.

Jagora : Ahayye yaro,

‘Yan Amshi : Ahayye yaro,

Jagora : Yaranaye kin ji kixan xan shana

:Yaranaye kin ji kixan xan shana

(Gusau, 1993:334-337).

Baya ga waxannan waqoqi na Malam Ashana mai ‘yan kamanci akwai waqoqi da dama waxanda suka shafi raha ga kuma ban dariya a adabin baka na Hausawa waxanda makaxa daban-daban suka aiwatar wato kamar ‘yan kama da ‘yan gambara da ‘yan galura da kuma ‘yan hoto da sauransu. (Gusau, 1993: 337).

Haka kuma akwai qagaggun labarai na raha waxanda Hausawa suka gudanar a gargajiyance, kuma suna daga sahun gaba wajen samar da nishaxi da annashuwa a zukatan jama’a, har wa yau kuma sukan zama sila ta qara danqon zumunci tare da cusa halin haquri ga jama’a kasancewar yadda ake dangata wani

qagaggen labari ga wata qabila kamar Fulani da Barebari da Nufawa ko Yarabawa da sauran su.

Wasu labaran na raha ba su da tushe wato babu gaskiya a labarin domin qirqiro su kawai ake yi, saboda sun qunshi jahilci ko wauta sai a danganta su da wasu qabilu musamman ma ga waxanda akwai wasa na zumunta a tsakaninsu domin nishaxi. Sai dai kuma akwai wasu labaran raha masu qanshin gaskiya a tare da su duk da cewa babu wani tabbaci a game da gaskiyarsu. Wato kamar labarin ‘yan doka na garin Daura waxanda aka ce “A lokacin da Turawa ke koya musu rawar fareti da harshen Turanci su kuma ba sa gane abin da ake faxa domin ba harshensu ba ne, saboda haka sai aka xaura musu tsumma a qafarsu ta hagu maimakon a ce “Left” “Right” wato (hagu dama), sai ana cewa “Mai tsumman marar tsumman, da haka har suka iya rawar faretin ‘yan doka. (Talle 1990: 25-26).

Haka kuma akwai labaran raha domin nuna yadda bambance-bambancen karin harshen Hausa yake ta fannin kalmomi da nahawu da kuma furuci wato daga wani lardi zuwa lardi ko daga yanki zuwa wani yanki wato kamar dai tsakanin Kanawa da Katsinawa ko tsakanin Sakkwatawa da Zagezagi kamar dai yadda wani Basakkwace ya je qasar Kano garin kalle-kalle ya ture wata yarinya mai tallar waina sai ta riqe shi ta na cewa “sai ka tsinan” wato ta na nufin sai ya tsince mata wainarta da ya zubar” shi kuwa bai fahimci abin da ta ke nufi ba, sakamakon bambancin karin harshensu.

Basakkwace ya dubi yarinya ya ce “Allah ya tsine maki” qarshe dai sai da jama’a suka shiga tsakaninsu aka sasanta su.

Har wa yau kuma akwai labaran raha a tsakanin qabilu inda ake nuna yadda wasu al'ummar wata qabila ke gudanar da rayuwarsu cikin wauta ko rashin wayewa wato kamar al'ummar Fulani da Barebari da Buzaye da Nufawa da Inyamurai waxanda Hausawa kan yi wa waxannan al'umma raha domin nishaxi saboda akan nuna ire-iren wautarsu ko rashin wayewarsu ko kuma wasu xabi'u marasa kyau, wato kamar labaran raha da Hausawa kan aiwatar ga al'ummar Fulani, domin nuna irin wautarsu da muguntar Fulani kamar yadda ya faru a labarin "Sai ya Kasanshe".

Wato wani Bafillatani ne ya ga mahaifinsa yana ja da baya da baya kuma akwai rijiya a bayansa wanda bai san da ita ba, sai xan nasa ya ce "Ga wani abu shan zai kasanshe, amma ba zan faxa ba sai ya kasanshe" da ya ga mahaifin nasa ya faxa rijiyar tunjum! Sai ya ce "Yo! Ya kasanshe".

Haka kuma akwai labarin mafarkin Buzu wanda wani Buzu ya yi mafarkin ya hau raqumi, sai ya je wajen wani malami domin ya fassara masa mafarkin da ya yi, ya ce "Malam na yi mafarki na hau raqumi" sai malam ya ce "A'a Alhamdulillahi, ai mafarki ne mai kyau domin ana nufin za ka shiga Aljanna" da Buzu ya ji haka sai ya ce "Sai na hau tozon" sai malam ya ce "Auzubillahi wuta za ka shiga" sai Buzu ya ce "Sai na sulmiyo" sai malam ya ce "Allahu Akhbar mutuwa za ka yi", sai Buzu ya ce "Sai na maqalqale" sai malam ya ce "To barkan ka".

Duk ire-iren waxannan labarai ana gudanar da su ne domin raha da kuma nishaxi kasancewar mafiya yawan labaran babu qanshin gaskiya a tattare da su, saboda haka ana yin su ne domin, a yi wa al'ummar da aka danganta ta da labarin

dariya tare da nuna wautarsu ko rashin wayewa ko kuma jahilci da sauransu. (Talle 1990: 49-53).

2.3.2 Raha A Rubutaccen Adabin Bahaushe

A nan za a yi qoqari ne wajen fito da raha, ko kuma bayyana yadda zantukan raha suka kasance a rubutaccen ayyukan adabin Bahaushe, wato kamar rubutattun waqoqin Hausa da qagaggun labaran Hausa da kuma rubutattun wasannin kwaikwayo na Hausa.

2.3.2.1 Raha A Qagaggun Labarai na Hausa

Qagaggen labari shi ne labarin da marubuci kan zauna ya qirqira ya kuma tsara labarin bisa jigon da yake son gina labarin a rubuce. Ire-iren waxannan labarai ba wai labarai ba ne na zahiri, illa kawai marubutan ne kan qago labaransu domin suna da saqo na musamman da suke son isar wa ga masu karatu. Ammam kuma wani lokaci sukan kwatanta labaransu da rayuwar al'umma ta zahiri, wanda ya shafi al'amuran yau da kullum. Haka kuma kusan duk qagaggen labarin da babu raha ko nishaxi a cikinsa yakan haifar da gundura ga masu karatu. Saboda haka, labari mai qunshe da raha da nishaxi kan jawo hankulan masu karatu wajen fahimtar saqon da ke qunshe da labarin.

Akwai fitaccen marubucin qagaggun labarai na Hausa masu qunshe da abubuwa na raha da sanya nishaxi, wato Alhaji Abubakar Imam wanda ya rubuta labarin *Ruwan Bagaja* a inda abubuwa na raha da ban dariya sukai ta faruwa a tsakanin Malam Zurqe da Alhaji Abubakar Imam. Kamar inda Malam Zurqe ya kore wa kashin Alhaji quda a birnin Manta lokacin da matar malam Zurqe ta taka wa Alhaji Abubakar qafa zai magana ta ce masa "Lebura ba wanda ya fi shi izza".

Shi kuma sai ya ce, “Ban yi sai da mijinki”. Ta dube shi da fushi ta ce “qarya ka ke yi”. Malam Zurqe ya fi ka, kar ka gama kanka da shi”, sai Alhaji Abubakar ya ce “Gobe da azahar, im ba qarya ba, mijinki ya tarshe ni a daji mana”.

Azahar na yi matar Malam Zurqe ta je gidan Alhaji Imam ta na zaginsa ta na cewa “Tashi mana mu je dajin”. Alhaji Imam ya ce “Mu je ina zuwa”.

Bayan ta koma gida ta zuga maigidanta har ya xauki kulki ya nufi daji ya na jiran Alhaji Imam ya zo a yi ta ta qare. Alhaji Imam ya nemi shuni ya shafa a fuskarsa ya nemi qotar gatari ya sava ya vullo musu ta baya yana tafiya yana zage-zage suna hangensa suka sha jinin jikinsu sai matar ta ce “Ga wani mahaukaci nan tafe”. Sai mijin ya waiga yana qyaqqyafta idanu. Ko da Alhaji Imam ya matsa kusa da su, sai ya kafe matar da mari har sau uku mijinta bai tanka ba sa’annan ya ce su kwance kayansu suka kwance jikinsu na rawa. Alhaji Imam zai bar su ya tafi saboda dariya ta turnuqe shi sai ya tuna da wani abin dariya wanda ya koma gefe ya yi kashi ya kira matar ya ce, “ki xauki kwano ki rinqa yi wa mijinki kixa, kai ko ka tsuguna nan ka riqa kore wa kashina quda domin idan ka bar quda ya ci mini kashi zan yanka ka”. Malam Zurqe ya ce, “To ranka shi daxe an gama”, ya tashi da rawar jiki ya sa hannu yana kore quda daga kan kashin Alhaji Imam

Matarsa kuwa ta xauki kwano tana yi masa kixa da waqa wai domin ya qara him ma ga aikin da Alhaji Imam ya sa shi.

Daga baya malam Zurqe da Alhaji Imam sun qara haxuwa a wani gari wai shi Miska a inda Malam Zurqe yake bai wa alhaji Imam labarin irin jan faxa na wannan matar tasa wai wata rana ta jawo wani qato faxa har ya mareta ko da ya

mare ta sai ta ruga ta faxa masa, nan da nan suka sheqa zuwa wajen qaton. Da ya isa ya dube shi ya ga ya kai qato sai ya ce “kai ka mari matata?” qaton ya amsa da fushi ya ce “Ni ne, ko za ka rama mata ne?”. Sai Malam Zurqe ya ce “qara marinta mu gani”, qaton nan ya dubi matar nan ya qara share ta da amri. Malam Zurqe ya ce “A’a da gaske kuwa ka ke yi? Qara marin ta mu gani”, qato ya qara duban matar ya share da mari har bakinta na jini, da malam Zurqe ya ga haka sai ya ce, “Tashi mu je, Allah ya rama mana”.

Bayan sun koma gida tana kuka sai ya ce, “Bari kuka, ai ko da ki ka gan ni nan kamar ban ce kome ba, daquwa nake masa ta cikin riga”.

2.3.2.2 Raha a Rubutattun Wasannin Kwaikwayo na Hausa

A vangaren rubutattun wasannin kwaikwayo akwai wasani da dama masu qunshe da zantuka na raha wato kamar wasan Tabarmar Kunya na Xandago, A. da Dauda Kano 1971.

Babban jigon wannan wasa shi ne faxakarwa da nishaxantarwa, dalili kuwa idan aka dubi irin sharholiya da barikanci da wasan ya qunsa, taurarin wasan kuwa sun haxa da Mantau da Salamatu matarsa sai qananan taurarin wasan su ne Idi abokin Mantau da Musa kurma qanin Mantau da suruki uban Salamatu da suruka uwar Salamatu, sai uwar kinibibi Fati Sabis a gidan giya da Yahaya xan gida Xan Daudu yaron Fati, sai yaro xan maqwabcin surukin Mantau.

Wannan wasa na Tabarmar kunya qunshe yake da raha da nishaxi domin Salamatu ta yi yaji ta koma gidan iyayenta, ba su mayar da ita ba, har sai da Mantau ya je biko gidan su Salamatu shi da qanensa Kurma da abokinsa Idi. A wannan lokaci na biko Mantau ya aikata wani abin kunya a gidan surukansa, wato

inda ya yi tumu a xakin surukansa kuma har ya kwanta a tsakiyar xakin surukan nasa. Bayan ya fahimci hakan ya bar gidan da gudu ya koma garin su.

Haka kuma a wasan Bora da Mowa na Umar Balarabe Ahmad wanda aka rubuta a shekara ta 1972. Jigon wasan shi ne faxakarwa da nishaxantarwa. Taurarin wasan kuwa su ne: Uiu – wani xan kasuwa da Abdu qanin Ilu da Habu abokin Ilu da Umma yarinyar da Ilu ke nema da aure da daudu wani dattijo shi ma manemin Umma ne da ziza matar Ilu ta biyu da Dogara xan Ziza da Ali Xan Umma da Madam Danlof wata mai otel sai ta Birni wata karuwa ce da Ido xaya wata mayya, kuma mai bayar da magani. Sai ‘yan sanda guda biyu da Malamai guda biyu da uban Umma da kuma uwarta.

Wasan na qunshe da raha da nishaxi idan aka dubi rayuwar Ilu da matarsa ta farko, wato Umma, da kuma yadda ya sake aure na biyu, wato Ziza kuma tsohuwar kilaki ce, saboda yadda ta rinqa juya Ilu kamar waina wanda haka ya jefa shi a wani hali. Sa’annan kuma ya dinga gallazawa matarsa ta farko ita da xanta Ali har suka bar gidan, suka bar shi da karuwa Ziza. Har dai Ziza ta shirya makirci domin ta kashe Ilu ta gaji dukiyarsa amma daga baya qaiqayi ya koma kan masheqiya domin Ziza ta rasa ranta da kuma xanta Dogara. A qarshe dai Ilu ya yi nadamar wannan al’amari a inda ya dawo da matarsa Umma da xanta Ali suka ci gaba da rayuwarsu.

Haka kuma akwai vurvushin raha a wasan Uwar Gulma na Muhammad Sada wanda ya rubuta a shekara ta 1971. wasan dai na xauke da taurari kamar malam Hayatu – wani masinjan gidan waya ne, Halima kuma matar malam Hayatu ce. Haka kuma akwai Uwar Gulma wata tsohuwa ce, sai Uban Ba’u wani

mai arziqi ne kuma mai bayar da bashi. Sa'annan kuma akwai Mudi yaron Uban Ba'u da Uwar Halima da malam Haruna Uban Halima da mama mai sayar da giya, kuma yarinyar Malam Hayatu. Har wa yau kuma akwai Dujal Xan Maho a gidan giya da mota malamin auduga, mai sayen giya da yaron Alqali da Alqali Dogari da kuma Muhuti.

Shi dai wannan wasa kusan a iya cewa an shirya shi ne domin raha da nishaxantarwa saboda malam Hayatu wani xan duniya ne, kuma mashayin giya, wanda hakan ke yawan haifar da samun savani a tsakaninsa da matarsa Halima, game da kuxin cefane. Wanda a kan haka wata rana malam Hayatu ya mari matarsa Halima, ita kuma ta yi masa duka da muciya, sa'annan kuma ta tafi gidan iyayenta da sunan yaji.

Bayan Halima ta gama faxawa iyayenta abubuwan da suke faruwa a tsakaninta da malam Hayatu, sai mahaifinta ya tafi wajen malam Hayatu domin ya tabbatar da abubuwan da Halima ta faxa masa, sai ya taras da Malam Hayatu a mashaya giya ya sha ya yi tatul yana tangaxi, sa'annan kuma ga karuwarsa Mama mai giya tana rungume da shi a qugu. A inda malam Hayatu ya umurci mahaifin Halima da shi ma ya zauna a kawo masa giya, sai surukin nasa ya ture shi, ya fita abinsa. Daga nan ya tabbatar da abubuwan da Halima ta faxa masa gaskiya ne.

2.3.2.3 Raha A Rubutattun Waqoqin Hausa

Marubuta waqoqin Hausa, wasu mutane ne da Allah (S.W.T) ya bai wa hikima da fasaha ga kuma basira da kaifin hankali domin sukan shirya waqa, su kuma tsara ta a rubuce domin isar da wani muhimmin saqo ga al'umma. Haka

kuma mawaqan sukan shirya waqa a kan abubuwa daban-daban kamar gargaxi da tarbiya ko faxakarwa da kuma wa'azi ko tarihi da sauran su.

Har wa yau kuma mawaqa kan yi amfani da wasu zavavvun kalmomi ko wasu zantuttuka na musamman domin samar da raha da nishaxi ga masu karanta waqoqin nasu. Wato kamar yadda aka samu ire-iren waxannan zantuka na raha a waqar 'Yar gagara (wato karuwa) ta Aqilu Aliyu. Ga yadda yake cewa a waqar:

Gara a kwara akwai ta da birki,
Cutar karuwa ba ta makanga,
Ga ta da fuska ba annuri,
Kar ka faxa mata wannan haske.
Ba ta da haske ban da na hoda,
Sai fankeke ka dan ta shafo.
Wannan ba a kira nasa haske,
Sai mu gaya masa qyallin banza.
(Fasaha Aqiliya, 1979:11).

A nan mawaqin ya yi amfani da wasu zavavvun kalmomi domin samar da raha da nishaxi ga makaranta ko sauraron waqar.

2.4 Ayyukan Da Suka Gudana Kan Aliyu Namangi

A nan ma an sami ayyukan da aka gudanar kan Aliyu Namangi. An samu kundayen bincike, da littattafai da kuma muqalu.

2.4.1 Kundaye

Xangambo (1973) ya gudanar da nazari kan rayuwar Aliyu Namangi da waqoqinsa. Ya kawo tarihin Aliyu Namangi, wato tun daga haihuwarsa har ya zuwa lokacin da ya fara wallafa waqoqin Hausa, ya kuma yi tsokaci kan yadda ya fara rubuta waqoqinsa tare da bayyana waqar da ya fara rubutawa, wato waqar "*Kanzil Azimi*". Har wa yau kuma ya bayyana yadda mawaqin ya rubuta waqar

‘*Imfiraji*’ a sanadiyar roqon da ‘yarsa ta yi masa da ya yi waqar, wacce ta tura kishiyarta Ajuji da ta gabatar da wannan buqatar ga mahaifinta, saboda kunya wacce take tsakanin xan fari da mahaifa bisa al’adar Bahaushe.

Wannan aiki na Xangambo (1973) na da alaqa ta kusa da wannan nazari domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan rubutattun waqoqi, kuma waxanda mutum xaya ya wallafa, wato Aliyu Namangi. Amma duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu, sun bambanta, domin kuwa shi ya nazarci mawaqin ne da waqoqinsa a nan kuwa za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Nazarin Xangambo (1973) bai hana Hassan (1973) gudanar da nasa aikin a kan Aliyu Namangi, domin kuwa shi ma ya yi nazarinsa ne kan rayuwar Aliyu Namangi da muhimman ayyukansa. A inda ya fara da kawo tarihin Aliyu Namangi da yadda ya fara wallafa waqoqinsa. Sa’annan ya bayyana sigogin waqoqi. Daga nan sai ya yi tsokaci kan wasu manyan ayyukan Aliyu Namangi kamar waqar *Imfiraji* ya kuma nazarci salo da jigo da zubi da tsari da salon sarrafa harshe duk a waqar *Imfiraji*.

Akwai alaqa ta qut da qut tsakanin wannan aiki da wannan nazari, domin kuwa duk suna magana ne kan rubutattun waqoqin Hausa, kuma duk a kan waqoqin mutum xaya, wato Aliyu Namangi. Sai dai duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu sun bambanta, domin kuwa shi ya nazarci Aliyu Namangi ne da wasu manyan ayyukansa. A nan kuwa za a nazarci wasu waqoqin Aliyu Namangi ne domin a fito da kalmomi ko jimloli na raha daga cikinsu.

Birniwa (1981), shi ma ya gudanar da bincikensa ne kan waqar I*mfiraji* juzu’i na 1-4 ta Aliyu Namangi. A wannan bincike an yi cikakken sharhi ne kan

juzu'i guda biyu cikin harshen Hausa da na Turanci. Manazarcin ya fara ne da kawo tarihin marubucin waqar *Imfiraji* wato Aliyu Namangi. Daga nan kuma sai ya yi tsokaci kan waqoqin a matsayinsu na madahu. Ya nazarci waqar *Imfiraji* juzu'i na xaya tare da kawo ratayenta da kuma yin bayanin wasu kalmomi masu tsauri da ke cikin waqar. Haka kuma ya yi irin wannan sharhi a waqar *Imfiraji* juzu'i na huxu. Har wayau kuma aikin nasa bai tsaya a nan ba, sai da ya fassara waxannan waqoqi da ya yi nazarinsu daga Hausa zuwa Turanci.

Wannan aiki na Birniwa (1981) na da alaqa ta kusa da wannan aiki domin kuwa dukkansu suna magana ne, a kan waqoqin mutum xaya, wato Aliyu Namangi. Amma duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu sun bambanta domin kuwa shi waqar "*Imfiraji*" ya nazarta, wannan kuwa zai nazarci wasu waqoqinsa ne domin a fito da raha daga cikinsu.

Shi kuwa Yakawada (1987) Tarken matanin waqar *Kanzil Azimi*, ta Aliyu Namangi ya yi. Ya yi wa waqar wadataccen tarke musamman ma dangane da abin da ya shafi jigonta da salon warwararta, da tsarinta da kuma salon sarrafa harshenta. Haka kuma ya kawo tarihin Aliyu Namangi da bayani kan karin waqoqinsa da kuma duba sarrafa harshe a cikin waqoqin. Har wayau kuma an yi bayani a kan kalmomi masu wuyar fahimta.

Aikin Yakawada (1987) tamkar Xanjuma ne da Xanjummai da wannan aiki, domin kuwa ya kawo tarihin Aliyu Namangi wanda a nan ma za a yi hakan. Haka kuma waqoqin da za a duba a wannan aiki ya kawo ratayen wasu daga cikinsu. Amma duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu, sun bambanta domin

kuwa shi ya karkata ne, ga tarken matanin waqar *Kanzil Azimi*. A nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Sa'adatu, A. (1995) ta gudanar da bincikenta ne a kan yabo da habaici a rubutattun waqoqin Hausa. A inda ta bayyana wanzuwar rubutattun waqoqi da jigoginsu, da hayayyafan sababbin jigogi. Daga nan sai ta yi tsokaci a kan yabo da habaici a rubutattun waqoqi, a inda ta yi cikakken sharhi kan wasu waqoqin yabo da habaici, kamar irin waqar *Tabarkoko* ta Aliyu Xan Sidi da waqar *Hawainiya* ta Tijjani Tukur Yola, da waqar *Sabuwar Nijeriya* ta Abubakar Ladan.

Har wayau kuma ta kawo waqar begen Annabi (S.A.W) a inda ta kawo waqar *Imfiraji* juzu'i na xaya ta Aliyu Namangi. Ta kuma sake kawo waqar *Tsarabar Madina* ta Aliyu Namangi.

Akwai alaqa tsakanin wannan aiki na Abdullahi (1995) da wannan nazari ta yin la'akari da misalan waxannan waqoqi da ta kawo domin kuwa dukkansu, waqoqin mutum xaya ya wallafa su, sai dai a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Sankalawa (2005) shi ma ya bi sahun Yakawada (1987) domin kuwa shi ma tarken wasu waqoqin Aliyu Namangi ya yi, wato waqar *Imfiraji* juzu'i na biyu (ta mutuwa) da kuma waqar *Imfiraji* juzu'i na huxu (ta iyaye) manazarcin ya fara ne da kawo tarihin rayuwar Aliyu Namangi daga nan sai ya yi bayanin jigon waqoqin tare da bayyana zubi da tsarinsu da salon sarrafa harshen waqoqin. Har wayau kuma ya kwatanta waqoqin biyu da wasu waqoqin Sani Yusuf Ayagi, wato *Waqar Bulaliya* (ta mutuwa) da waqar xan'uwa-ma-ba-da-mama (ta iyaye).

Wannan aiki na Sankalawa na da dangantaka da wannan nazarin domin kuwa duk suna magana ne, a kan waqoqin Aliyu Namangi. Sai dai shi ya kwatanta waqoqin ne, da wasu waqoqin Sani Yusuf Ayagi. Wannan kuwa za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Duk da cewa Birniwa (1981) ya nazarci waqar "*Imfiraji*" hakan bai hana Nafisa, N. (2011) ta gudanar da nata nazarin ba kan waqar *Imfiraji* ba, domin kuwa ita ma ta nazarci waqar *Imfiraji* juzu'i na xaya ta fuskar fito da kalmomin Larabci da ya yi amfani da su a cikin waqar, kuma ta yi nazarin nata ne cikin harshen Larabci, a inda ta fito da ire-iren waxannan kalmomi na Larabci da ya yi amfani da su kamar irin su, Majidi, da Hamidi, da Yaumal Mi'adi, da Jadidi, da nifaqa, da ijaba, da Xaiba, da turba, da hilafa, da jahala, da istingifari da dai sauran su.

Wannan nazari na da dangantaka ta kusa da wannan aiki domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan waqoqin da mutum xaya ya wallafa, wato Aliyu Namangi sai dai sun bambanta domin kuwa a nan za a duba raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Muhammad (2011) ya gudanar da bincikensa kamar yadda Sankalawa (2005) ya kwatanta waqoqin Aliyu Namangi da na Yusuf Ayagi, shi ma ya kwatanta waqar *Jiddul Ajizi* (qwazon Gajiyayye) ta malam Shitu Xan Abdurra'uf da waqar *Kanzil Azimi* (Babbar Taska) ta Malam Aliyu Namangi. Manazarcin ya fara ne da bayyana tarihin mawallafan da kuma yadda suka fara wallafa waqoqin Hausa, da waqoqin da suka fara wallafawa. Daga nan sai ya xauki waxannan waqoqi da ya kwatanta su ya yi tsokaci a kansu ta hanyar sharhi dangane da salo

da zubi da tsari da salon sarrafa harshe. Daga nan sai ya kwatanta inda suka yi kama da juna da inda suka bambanta da juna.

Alaqar wannan nazari da wannan aiki ita ce, ya kawo tarihin rayuwar Aliyu Namangi da ayyukansa, da kuma waqar da ya fara rubutawa wanda a nan ma za a yi hakan. Amma duk da wannan alaqa da ke tsakaninsu sun bambanta domin kuwa shi waqar Aliyu Namangi ya xauka ya kwatanta ta da wata waqar, wannan kuwa za a xauki wasu waqoqi ne daga cikin waqoqin Aliyu Namangi domin fito da kalmomi ko jimloli na raha daga cikin su.

2.4.2 Littattafai

Namangi (1962) ya wallafa waqoqin *Imfiraji* juzu'i na xaya zuwa na huxu. A cikin littafin an kawo waqoqin ne tun daga waqa ta xaya zuwa waqa ta huxu kowacce waqa ta cika qa'idojinta na rubutacciyar waqa, wato mabuxi da marufi. Har wayau kuma kamar yadda aka bayyana a farkon littafin cewa an samu waqoqin ba cikakku ba, kuma a cike da kurakurai sai da aka koma wajen mawallafin ya gyara su suka zama cikakku. Har wayau kuma mawallafin ya sake wallafa littafi na biyu a shekarar (1972), wato waqar *Imfiraji* juzu'i na biyar zuwa na tara, wato waqa ta biyar zuwa ta tara kenan kamar yadda littafin farko ya kasance haka ma na biyun yake.

Baya ga waxannan littattafai na waqoqin *Imfiraji* juzu'i na xaya zuwa na huxu da juzu'i na biyar zuwa na tara, ya sake wallafa wani littafin a shekara ta (1972) mai xauke da waqar *Furan Gero* da waqar *Tsarabar Madina*.

Duk waxannan littattafai suna da alaqa ta kusa da wannan aiki domin kuwa duk mawallafin waqoqin mutum xaya ne, wato Aliyu Namangi. Sai dai a

nan za a nazarci wasu waqoqin Aliyu Namangi ne domin a fito da kalmomi ko jimloli na raha daga cikinsu.

Xangambo (1979) ya wallafa wani littafi mai xauke da wasu zavavvun waqoqin wasu mawallafa waqoqin Hausa. Ya fara ne da bayyana tarihin rubuta waqa a qasar Hausa daga nan sai ya yi tsokaci kan waqoqin qarni na sha tara da kuma waqoqin qarni na ashirin. Daga nan kuma sai ya yi bayanin yadda mawaqa ke tsara waqoqinsu da amfanin wasu waqoqi daga cikin waqoqin na qarni na goma sha tara da na ashirin daga cikinsu har da waqar *keke* ta Aliyu Namangi da waqar Zambon *Qazama* ita ma ta Aliyu Namangi ce. Wannan littafi yana da nasaba da wannan nazari kasancewar ya kawo waqoqin Aliyu Namangi har guda biyu kuma suna daga cikin waqoqin da za a nazarta a wannan nazari. Sai dai za a nazarci raha ce, a cikin waqoqin.

Shi kuwa Muhammad (2010) ya kawo tarihin Aliyu Namangi ne tun daga haihuwarsa har ya zuwa lokacin da ya yi aure da neman iliminsa da ayyukansa, wato har dai ya zuwa lokacin da ya fara wallafa waqoqi, da bayanin rayuwarsa da iyalansa har ya zuwa ranar da ya bar Duniya.

Akwai dangantaka tsakanin wannan littafi na Muhammad (2010) da wannan aiki domin a nan ma za a bayyana taqaitaccen tarihin Aliyu Namangi, amma duk da wannan dangantaka sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

2.4.3 Muqalu

Skinner (1969) ya gabatar da wata muqala wacce take xauke da bayanai kan tarihin rayuwar Aliyu Namangi, kama daga haihuwarsa har ya zuwa karance-karancensa da waqar da ya fara wallafawa a rayuwarsa wato waqar "*Kanzil Azimi*". Har wa yau kuma ya yi sharhi kan waqarsa ta "*Imfiraji*". Ya kuma xauki waqar "*Basukur*" ya yi mata sharhi, sa'annan kuma ya rubuta waqar da harshen Ingilishi tare da yi mata sharhi cikin harshen Ingilishi.

Wannan muqala tana da alaqa ta qut da qut da wannan nazari, domin kuwa dukkan waqoqin mutum xaya ne ya wallafa su, wato Aliyu Namangi. Har wayau kuma ita waqar *Basukur* da ya xauka ya yi mata sharhi tana daga cikin waqoqin da za a nazarta a wannan aiki. Sai dai shi ya nazarci waqar ce ta fuskar yanayin tsarinta da salon waqar. A nan kuwa za a nazarci waqar ce domin a fito da zantuka na raha daga waqar.

Malumfashi (1984) ya qalubalanci masana da suka bayyana cewa rubutattun waqoqin qarni na ashirin waqoqi ne na Duniya, ya yi wannan suka ne a takardar da ya gabatar wato "wa'azi a rubutattun waqoqin qarni na ashirin". Ya kawo ra'ayoyin masana dangane da waqoqin qarni na sha tara da na ashirin. Haka kuma ya kawo hujjoji da yake ganin su ne dalilan da suka sa waxannan masana suka taqaita jigon addini ga waqoqin qarni na sha tara. Daga cikin dalilan da ya kawo ya ce yi wa addinin Musulunci Banasariyar fahimta ce, wato taqaita ma'anar addini ga al'amuran lahira kawai ko kuma rarrabewa tsakanin al'amuran Duniya da na lahira. Daga nan sai ya bayyana waqoqin da ake iqirarin 'yan Duniya ne wato kamar waqar *Qazama* ta Aliyu Namangi da waqar *Basukur* ita ma

ta Aliyu Namangi, da waqar *'Yanci* ta Sa'adu Zungur da dai sauransu. Duk waxannan waqoqi yana ganin ba abin da ya raba su da waqoqin addini.

Akwai alaqa da ke tsakanin wannan muqala da wannan aiki kasancewar ya kawo waqoqin Aliyu Namangi har guda biyu wato Waqar *Qazama* da waqar *Basukur* kuma suna daga cikin waqoqin da za a nazarta a wannan aiki domin fito da raha daga cikinsu.

Shi kuwa Muhammad (1985) a muqalar da ya gabatar ya kawo misalan wuraren da Aliyu Namangi ya yi amfani da kalmomi waxanda ke nuna kamar yana gani, ko kuma ya tava gani. An gabatar da muqalar ce dangane da waqar *Tabuka* ta Audu Makaho da kuma waqar *Imfiraji* ta Aliyu Namangi.

Dangantakar da ke tsakanin wannan muqala da wannan nazari ita ce dukkansu suna magana ne, a kan mutum xaya, wato Aliyu Namangi, kuma shi ne mawallafin waqar *Imfiraji* wacce tana xaya daga cikin waqoqin da aka nazarta a muqalar. Amma a nan kuwa za a nazarci wasu waqoqi ne daga cikin waqoqin Aliyu Namangi domin a fito da raha daga cikin su.

Yakawada (1986) ya nazarci jigogin madahu ne, da jigogin sira a waqoqin Aliyu Namangi wanda ya rubuta domin sharar fagen gudanar da bincike na neman takardar shaidar digiri na biyu. Ya kawo rabe-raben rubutattun waqoqin Hausa amma a taqaice, ya kuma bayyana ma'anar madahu da sira, sannan kuma ya kawo nau'o'in madahu da na sira tare da bayyana tarihin samuwarsu.

Alaqar wannan aiki da wannan nazari ita ce, manazarcin ya nazarci jigon madahu ne, da sira duk a cikin waqoqin Aliyu Namangi. A nan ma waqoqin Aliyu

Namangi ne za a nazarta. Sai dai za a nazarci wasu waqoqi ne daga cikin waqoqinsa domin a fito da raha daga cikin su.

2.5 Ayyukan da suka Gudana kan Raha

An sami ayyukan da suka gudana kan raha. An samu waxansu ayyukan ne, a matsayin littattafai, wasu a matsayin kudanyen bincike, wasu kuwa a matsayin muqalu ko qasidu.

Waiwayen ayyukan na da matuqar muhimmanci ga wannan nazari domin qara samun haske ga wannan aiki.

2.5.1 Kundaye

Katsina (1984) ya gudanar da bincike dangane da muhimmancin labaran raha a wurin Hausawa. Manazarcin ya nuna cewa labarai irin na raha labarai ne da kan haifar da nishaxi ga jama'a. Har wa yau kuma ya kawo misalan labaran raha na Hausa da tatsuniyar gizo da qoqi da wasanni irin na 'yan kama da 'yan kacakaura da 'yan gambara da wawan sarki da kuma 'yan kashin kasuwa, da dai sauransu. Daga nan sai ya bayyana waxannan labarai da wasanni na raha suna da muhimmanci ga rayuwar Bahaushe domin sukan nishaxantar da shi bayan an kammala aikace-aikacen gida. Har wa yau kuma sukan haifar da kwanciyar hankali ga wanda yake cikin wata damuwa.

Alaqar wannan aiki da wannan nazari ita ce, dukkansu suna magana ne kan raha, sai dai shi ya kalli raha ce, a cikin labarai da muhimmancinta ga

al'ummar Hausawa. A nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Xahiru (1986) ya nazarci zantuttukan hikima ne na Muhammadu na Almamowa Funtuwa, a inda ya kawo taqaitaccen tarihinsa da tasirin zantuttukan Almamowa ga al'ummar Hausawa. Ya kuma kawo nishaxi da raha a matsayin su ne ginshiqan waxanan zantuttukan hikima na Almamowa. Ya kuma nuna cewa ta fuskar nishaxi da raha ce za a iya kallon waxannan zantuttukan hikima, a inda shi Alimamowa kan kwaikwayi wasu abubuwa don sa masu sauraronsa dariya, wato kamar kukan dabbobi, da kwaikwayon sautin wasu kayan kixa da sauran su.

Akwai dangantaka tsakanin wannan nazari da wannan aiki domin kuwa dukansu suna magana ne a kan raha sai dai shi ya kawo rahar ce a matsayin misalai. A nan kuwa rahar ce, za a nazarta ta hanyar fito da kalmomi ko jimloli na raha a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Aikin Talle (1990) da Xahiru (1986) tamkar Xanjuma ne da Xanjummai, domin kuwa Talle (1990) ya nazarci wasu aikace-aikacen hikimomin Muhammadu Almamowa Funtuwa a inda shi ma ya kawo taqaitaccen tarihinsa tare da bayanin yadda ya ke gudanar da harkokinsa na 'yan kamanci, domin nishaxantar da jama'a.

Haka kuma ya kawo bayanai da dama dangane da abubuwan da suka shafi labaran raha wato tun daga asalin labaran raha da nishaxi da ire-iren labaran raha da dai sauransu. Ya kuma nuna cewa su labaran raha ba su da wasu qa'idoji ko dokoki dangane da masu yin sa ko lokacin yin su. A inda ya kawo misali da

tatsuniya yake cewa “Ana cewa “Ba a yin tatsuniya da rana sai an xaure Gizo idan ba haka ba kuwa mutum zai yi makuwa”.

Wannan aiki yana da dangantaka da wannan nazari, domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan rahar sai dai shi ya kalli rahar ce ta fuskar zantuttukan hikima na Muhammadu Almamowa Funtuwa. A nan kuwa za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Shi kuwa Zubairu (1992), ya nazarci raha ce a wasan kwaikwayon Hausa, ya kawo ma’anar wasan raha da cewa “wasa ne da ke haifar da nishaxi da ban dariya ga ‘yan kallo. Har wayau kuma ya yi bayanin ire-iren kayan ‘yan wasan raha da yadda suke magana a cikin wasan da dai sauransu.

Dangantakar wannan aiki da wannan nazari ita ce raha, sai dai shi ya kalli rahar ce, a wasan kwaikwayon Hausa. Wannan kuwa za a nazarci rahar ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Sani (1992), ya nazarci raha ce a tsakanin waxanda wasa ke wakana a tsakaninsu a dalilin sana’o’insu. Ya kawo misalai da masu sana’ar kifi da mahauta da dai sauransu.

Wannan nazari na da alaqa da wannan bincike domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan raha, sai dai shi ya kalli rahar ce a mutanen da wasa ke wakana a tsakaninsu a sanadiyyar sana’o’insu. A nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Iliyasu (1995) ya gudanar da nazarinsa ne kan raha da gaskiya cikin labarin *Ruwan Bagaja*. A inda ya fara da kawo tarihin samuwar littafin *ruwan bagaja*, da tarihin mawallafin. Daga nan sai ya yi tsokaci dangane da gaskiya a

cikin littafin, bayan nan kuma sai ya bayyana wuraren da aka yi amfani da maganganu ko kalmomi na raha a cikin littafin.

Wannan aiki na da alaqa da wannan nazari, kasancewarsu duk suna magana ne kan raha, sai dai shi ya kalli rahar ce, a labarin *Ruwan Bagaja,* a nan kuwa za a kalli rahar ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Baya ga Zubairu (1992), ya nazarci raha a wasan kwaikwayo na Hausa, hakan bai hana Isa (2007) da Abubakar (2009) da Aminu (2012) su ma sun nazarci raha a wasan kwaikwayon Hausa, sai dai zaman ‘yan marina aka yi wato kuwa da inda ya dosa.

Yayin da Isa (2007), ya nazarci raha a wasan kwaikwayon Hausa ta fuskar tarken wasannin Karambana. A inda ya kawo taqaitaccen tarihinsa da samuwar wasannin da ire-iren wasannin Karambana, ya kuma kawo misalan wasu wasannin Karambana.

Shi kuwa Abubakar (2007) ya nazarci raha ce, a rubutaccen wasan kwaikwayon Hausa. Wanda ya yi kan wasan *Malam Inkuntum*.

Musa (2008), shi ma ya nazarci raha ce, a wasan kwaikwayon Hausa amma shi sai ya yi sharhi kan wasan *Shiga Sharo ba Shanu* na gidan talabijin na N.T.A, Kaduna.

Sambo (2009), kuwa ya nazarci yadda wasan kwaikwayon raha ya bunqasa ne, ta gudummuwar Shehu Jibrin Golovo. Ya yi tsokaci a kan rukunan mutanen da suke bayar da gudummuwa ga wasan raha a qasar Hausa kamar irin su ‘yan gambara da ‘yan garura. Har wayau kuma ya kawo bayanai dangane da

raha cikin rubutaccen adabi a inda ya kawo misalai da qagaggun labarai da rubutaccen wasan kwaikwayo da dai sauransu.

Shi kuwa Aminu (2010), ya nazarci raha ce a wasan kwaikwayon Hausa ta fuskar kwatanta wasannin Karambana da na Xan Ibro. Ya bayyana manufa da ma'anar wasan raha da siffofin wasan raha da yanaye-yanayen wasan raha. Har wayau kuma ya kawo misalan wasannin raha a rediyo da na talabijin da kuma gidajen rediyon da ake gudanar da kowanne wasa.

Haqiqa duk waxannan aikace-aikace suna da alaqa ta kusa da wannan nazari domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan raha, sai dai su, sun fi mayar da hankali ne a kan raha ta fuskar wasannin kwaikwayo na Hausa. A nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

2.5.2 Littattafai

Meredith (1977) ya wallafa littafi a kan wasan raha, a inda ya bayyana ma'anar wasan raha da cewa "wasan raha dole ne ya kawo wa mutane nishaxi domin maqasudinsa shi ne mamaye zuciya da annashuwa da raha ga mai sauraro ko kuma xan kallo. Har wayau kuma ya kawo yanaye-yanayen wasan raha da siffofin wasan raha.

Wannan littafi na da dangantaka da wannan aiki, sai dai shi ya kalli raha ce, a wasan kwaikwayo, kuma ya wallafa littafin cikin harshen Turanci ne, a nan kuwa za a gudanar da nazarin ne cikin harshen Hausa. Kuma za a kalli rahar ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Crow (1983), ya wallafa littafi kan wasan kwaikwayo, ya kuma kawo ire-iren wasan kwaikwayo daga ciki har da wasan raha wanda ya nuna cewa shi ne kan gaba da sauran wasannin kwaikwayo. Har wayau kuma ya kawo sigogin wasan da siffofin wasan kwaikwayo na raha da kuma wuraren da ake gudanar da wasan kwaikwayo na raha da tufafinsu da ire-iren kalamansu a lokacin gudanar da wasan kwaikwayon na raha.

Akwai dangantaka tsakanin wannan littafi da wannan nazari duk da cewa ya wallafa littafin cikin harshen Ingilishi.

Domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan raha, sai dai shi ya kalli raha ce, ta fuskar wasan kwaikwayo, wannan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Stephen (2006), ya wallafa littafinsa ne kan adabin Ingilishi, wato ya yi maganganu da yawa dangane da adabi, ciki har da magana kan raha a inda ya bayyana ma'anar wasan raha da cewa "Ana sarrafa kalmar wasan raha da dukkan wani abu da ke iya sa mai karatu ko xan kallo dariya". Haka kuma ya bayyana yadda wasan raha yake a jiya da kuma yau. Ya kuma kawo nau'o'in wasan raha da siffofin wasan raha da yanaye-yanayen wasan raha da dai sauransu.

Dangantakar wannan littafi da wannan nazari ita ce, dukkansu suna magana ne, kan raha, sai dai shi ya nazarci raha ce, a wasan kwaikwayo. A nan kuwa za a duba raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Waxannan su ne aikace-aikacen da wannan nazari ya ci karo da su, kuma hannu ya kai gare su, waxanda suke da alaqa ta kusa ko ta nesa da wannan nazari.

Waxannan ayyuka da aka duba na magabata sun taimaka qwarai wajen haskaka alqiblar wannan aiki.

Da ma kuma Hausawa kan ce “Da na gaba ake gwada zurfin ruwa”.

2.6 Ayyukan Da Suka Gudana Kan Rubutattun Waqoqin Hausa

Masana da manazarta daban-daban sun gudanar da aikace-aikace da dama a wannan fage na rubutattun waqoqin Hausa, sai dai kowanne manazarci da inda ya dosa wato kowa da abin da ya nazarta daga rubutacciyar waqar Hausa.

Domin kuwa wasu sun xauki wasu waqoqi ne suka kwatanta su da wasu waqoqin wasu kuwa sun gudanar da nazarinsu ne kan wani mawallafin wasu waqoqi da dai sauran vangarori da akan iya dubawa domin nazartar rubutacciyar waqar Hausa. Saboda haka ya dace a duba ire-iren waxannan ayyuka da suka gudana kan rubutacciyar waqar Hausa domin qara samun haske da kuma inganta wannan aiki.

2.6.1 Kundaye

Waxansu daga cikin ayyukan da aka gudanar kan rubutattun waqoqin Hausa a matsayin digiri na xaya da na biyu da na uku sun haxa da Sa’id (1978) da Xangambo (1980) da Yakasai (1984) da Dunfawa (1990) da Birnin-Tudu (1992) da Sa’id (2002) da Dunfawa (2002) da Auta (2008).

Sa’id (1978) ya gudanar da bincikensa ne kan salo da tsarin rubutacciyar waqar Hausa a qarni na goma sha tara (19). Ya yi bayanin yadda tsarin waqoqin Hausa suke ta fuskar salo a wannan qarni na goma sha tara (19). Haka kuma ya kawo tarihin rayuwar wasu masu jihadi tare da bayyana ire-iren gudummuwar da suka bayar wajen gudanar da jihadi ta fuskar wallafe-wallafen waqoqi domin

faxakarwa, sannan kuma ya yi sharhi game da jigo da tsari da salon waqoqin da masu jihadin suka wallafa a qarni na goma sha tara (19).

Wannan aiki na Sa'id (1978) ya na da alaqa da wannan nazari kasancewarsu duk suna magana ne game da rubutacciyar waqar Hausa sai dai duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci wasu waqoqin Aliyu Namangi ne domin a fito da zantukan raha daga cikinsu.

Xangambo (1980) wannan bincike ya gudana ne kan waqoqin Musulunci na Hausa masu jigon wa'azi a inda binciken ya tabbatar da cewa dukkan waqoqin Musulunci wa'azi suke xauke da shi, amma duk da haka sai aka kasa su zuwa kashi-kashi wato wa'azi bakandame wanda ya haxa komai da komai daga nan kuma sau bayanin tuna mutuwa da kuma sauran ayyuka na ibada.

Binciken na Xangambo (1980) na da dangantaka da wannan aiki ta yin la'akari da dukkansu suna magana ne kan rubutattun waqoqin Hausa, kuma waqoqin da aka nazarta kusan jigonsu xaya ne wato wa'azi, amma duk da wannan dangantaka da ke tsakaninsu sun bambanta domin a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Shi kuwa Yakasai (1984) ya gudanar da bincikensa ne kan rayuwa da wasu aikace-aikacen Alqali Na'ibi Suleiman Wali ya gudanar a lokacin rayuwarsa a inda ya fara da bayyana tarihin rayuwarsa tun daga haihuwarsa har ya zuwa girmansa, da neman iliminsa, sannan ya bayyana wasu aikace-aikacensa kamar rubuce-rubuce ciki har da wasu waqoqin Hausa da ya wallafa.

Wannan aikin na da alaqa da wannan bincike kasancewar duk sun tavo magana kan rubutattun waqoqin Hausa tare da taqaitaccen bayani kan mawallafan, amma duk da wannan alaqa sun bambanta domin kuwa shi ya nazarci wasu ayyukan Alqali Na'ibi Suleiman Wali ne, a nan kuwa za a nazarci raha ce daga wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Dunfawa (1990) ya nazarci gudummuwar masu xariqa wajen kawo ci gaba da havvakar rubutattun waqoqin Hausa, bincike ya fi ba da muhimmanci ne ga fitattun xariqun Tijjaniyya da qadiriyya tare da kawo tarihin wanzuwarsu a qasar Hausa.

Manazarcin bai tsaya a nan ba sai da ya xauki jigogin waqoqin nasu ya yi sharhi a kansu sannan kuma ya yi tsokaci kan irin tasirin da waqoqin ke da shi da kuma tsarin waqoqin.

Wannan aiki na Dunfawa (1990) ba zai rasa dangantaka da wannan aikin ba domin kuwa duk suna magana ne a kan rubutattun waqoqin Hausa kuma dukkansu kusan waqoqi ne da suke magana kan addini ta fuskar wa'azi da yabon Annabi (S.A.W).

Amma duk da wannan dangantaka suna da bambanci da wannan aikin domin kuwa a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Shi ma Birnin-Tudu (1992) ya nazarci jigo da salon rubutattun waqoqin furu'a ne na qarni na ashirin, a inda ya nazarci ire-iren waxannan waqoqi ta fuskar fito da jigonsu sannan kuma sai ya yi tsokaci game da irin salon da aka yi amfani da shi wajen gina waqoqin, har wa yau kuma ya kawo tubalan ginin arulin Hausa da kuma irin sauye-sauyen da akan samu cikin karuruwan arulin Hausa. Haka

kuma ya yi tsokaci kan shigowar addinin Musulunci qasar Hausa sa'annan kuma sai ya bayyana yadda qasar Hausa ta ke kafin shigowar addinin Musulunci, har wa yau kuma ya kawo ma'anar waqa da tarihin samuwar waqa sai a qarshe ya yi bayanin samuwar ilimin furu'a a qasar Hausa da ma'anar furu'a da kuma yadda ilimin furu'a ke da tasiri a wajen malaman qasar Hausa. Sa'annan kuma ya nazarci wasu waqoqin furu'a kamar waqar *Sallah* ta Balarabe Shehu Illela da kuma waqar *Rabon Gado* ta Farfesa Aliyu Gwandu.

Wannan aiki na da dangantaka da wannan bincike kasancewar dukkansu suna magana ne kan rubutattun waqoqin Hausa sai dai shi ya nazarci waqoqin furu'a ne, a nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Satatima (1999) ya nazarci yadda rubutattun waqoqin Hausa suka yi tasiri a kan adabin baka, a inda ya binciko yadda marubuta waqoqin Hausa kan yi amfani da wasu sassa na adabin baka kamar qissa da tatsuniya da hikaya da tarihi a cikin waqoqinsu.

Haka kuma ya kawo ma'anar adabi da rabe-rabensa, har wa yau kuma ya yi tsokaci dangane da samuwar rubutacciyar waqar Hausa wato tun daga qarni na goma sha bakwai (17) zuwa qarni na goma sha takwas (18) da kuma qarni na goma sha tara (19) tare da bayyana ire-iren jigogin da aka rinqa samu a waxannan lokuta.

Alaqar wannan nazari da aikin Satatima (1999) ita ce dukkansu suna magana ne kan rubutacciyar waqar Hausa, sai dai duk da wannan alaqa da ke tsakaninsu sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Dunfawa (2002) ya gudanar da bincike game da dangantakar da ke tsakanin yara da waqa ta baka da rubutacciyar waqa a inda ya fara da bayyana su wane ne yara tare da yin tsokaci kan xabi'unsy da kuma irin alaqar da ke tsakaninsu da waqa. Daga nan kuma sai ya kawo tarihin samuwar waqoqin yara na baka da rubutattu tare da bayyana ire-iren amfaninsu ga yara sannan kuma ya kawo sigogin da waqoqin yara ke da su, haka kuma ya yi sharhi kan nau'o'in waqoqin yara da masu shirya su da aiwatar da su da lokutan tare da wuraren sadar da su. Har wa yau kuma ya nazarci jigogin waqoqin yara da ma'auninsu na tsantsar Hausa da ararru daga Larabci, sai a qarshe ya yi tsokaci kan zubi da tsari da salon sarrafa harshe na waqoqin, bayan nan sai ya zavi wasu waqoqin baka guda huxu na yara ya yi sharhi a kan kowaccensu.

Alaqar da ke tsakanin wannan aiki na Dunfawa (2002) da wannan bincike shi ne duk suna magana ne a kan waqoqin Hausa a inda shi ya fi mayar da hankali ne ga waqoqin baka na yara, a nan kuwa za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Sa'id (2002) ya gudanar da bincikensa kan rubutattun waqoqin Hausa ne na qarni na ashirin amma jihohin Sakkwato da Kabi da Zamfara a inda ya fara da tsokaci kan irin dangantakar da ke tsakanin rubutacciyar waqa da waqar baka, da irin gudummuwar da rubutun Ajami da na boko suka bayar wajen yaxuwa da bunqasar waqoqin Hausa, sannan kuma ya yi bayanin rubutattun waqoqin Hausa a qarni na goma sha tara (19) da na ashirin (20) wato dangane da irin gudummuwarsu ga jama'a.

Haka kuma ya zavi wasu fitattun marubuta waqoqin Hausa goma sha biyu daga shiyyar waxannan jihohi na Sakkwato da Kabi da Zamfara, a inda ya kawo tarihin rayuwarsu, sannan kuma sai ya kawo jerin sunayen wasu mawaqan goma sha bakwai ‘yan asalin wannan shiyya, daga nan sai ya shiga bayani kan jigogin rubutattun waqoqin Hausa na marubutan yana mai yin sharhi tare da misalai daga wasu waqoqinsu, sai kuma ya nazarci salo da tsarin rubutattun waqoqin Hausa na qarni na ashirin a wannan shiyya ta Sakkwato da Kabi da zamfara.

Akwai dangantaka a tsakanin wannan nazari na Sa’id (2002) da wannan aiki kasancewarsu duk suna magana ne kan rubutacciyar waqar Hausa ne, sai dai sun bambanta domin a nan za a nazarci wasu waqoqi ne na Aliyu Namangi domin a fito da zantuka na raha daga cikin su.

Shi ma Auta (2008) ya bi sahun Sa’id (2002) da Habibu (2001) domin kuwa ya nazarci rubutattun waqoqin Hausa na faxakarwa a qarni na ashirin, a inda ya nazarci babban jigon waqoqin faxakarwa tare da sauran wananan jigoginsu sannan kuma sai ya raba qananan jigogin zuwa manyan rukunan wayar da kai da na zamantakewa, daga nan sai ya yi wa wasu waqoqin sharhi mai gamsarwa a matsayin misalai.

Alaqar wannan aiki na Auta (2008) da wannan bincike shi ne dukkansu suna magana ne dangane da rubutacciyar waqar Hausa, sai dai sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

2.6.2 Littattafai

Akwai wallafaffun littattafai da dama da aka buga masu dangantaka da wannan aiki ta fuskar waqa, inda wasu suke Magana kan rubutattun waqoqin

Hausa wasu kuwa suna Magana ne kan waqoqin baka na hanyoyin nazarin waqa rubutacciya ko ta baka, ko ma duka biyun, wato kamar dai yadda Sarvi (2007) da Gusau (2008) da Xangambo (2008) duk sun yi nazari kan rubutacciyar waqa da ta baka sai dai kowa da inda ya kalla domin kuwa:

Sarvi (2007) ya wallafa littafinsa ne kan yadda ake nazarin waqoqin Hausa, a inda ya yi bayanin ma'anar rubutacciyar waqa ya kuma nuna cewa babu wata sahihiyar ma'ana da masana suka bai wa waqa, sai dai abin da marubuta suka fi yi shi ne sukan ti la'akari ne da abubuwan da waqa ta qunsa wajen bayar da ma'anarta. Daga nan kama sai ya bayyana nau'o'in waqoqin Hausa kamar irin su gwauruwa, qwar xaya da makamantansu, sa'annan kuma ya duba ma'aunin waqa, mabuxi da marufi da jigo wato yadda ake gano jigon waqa. Sa'annan kuma sai ya yi tsokaci kan salo da sarrafa harshe, haka kuma ya nuna yadda ya kamata a yi nazarin waqa sosai.

Wannan littafi na Sarvi (2007) na da alaqa da wannan nazari kasancewarsu duk suna magana ne a kan rubutacciyar waqar Hausa sai dai a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Gusau (2008) ya gudanar da nasa nazarin ne kan waqoqin baka na Hausa a inda ya duba yanaye-yanayensu da sigoginsu, sannan kuma ya zirfafa nazari kan waqoqin baka, domin a cikin littafin ya kawo ire-iren waqoqin baka ciki har da waqoqin ban dariya na baka tare da bayyana masu gudanar da ire-iren waxannan waqoqi wato kamar 'yan kama da 'yan gambara da kuma 'yan kacakaure. Har wa yau kuma mawallafin ya yi tsokaci kan samuwar waqoqin a qasar Hausa.

Duk da cewa aikin nasa a waqoqin baka ya gudana, amma akwai alaqa da wannan nazari domin kuwa dukkansu suna magana ne kan waqoqin Hausa kuma ya kawo waqoqin ban dariya masu ratsin raha a cikin su. Amma duk da wannan dangantaka da ke tsakanin su, sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Xangambo (2008) ya nazarci manyan hanyoyin nazari da sharhin waqa, a inda ya nazarci hanyar nazarin ta gargajiya da ta zamani, duk da cewa ya nuna hanyar nazarin gargajiya ba wata fitacciyar hanya ba ce da aka tsara, amma hanyar nazari ta zamani ta haxa da hanyar nazari ta gargajiya da ta Larabawa da kuma ta Turawa.

Mawallafin ya kawo abubuwa muhimmai da ake dubawa a lokacin nazarin waqa wato kamar su jigo, da salo, da zubi, da tsari da makamantansu.

Alaqar wannan aiki da wannan nazari dukkansu suna magana ne a kan waqa, sai dai a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Baya ga masanan da suka wallafa littattafai game da hanyoyin nazarin waqoqin Hausa, akwai kuma waxanda suka gudanar da nazarin ko sharhi kan wasu waqoqi wato kamar irin su:

C.N.H.N (1977) da Xangambo (1979) da C.N.H.N (1979) da Diji (2004) da Mukhtar (2005) duk wasu waqoqin Haisa ne suka yi wa sharhi.

C.N.H.N. (1977) littafin ya qunshi cikakken sharhi da masana suka yi ne a kan rubutattun waqoqin Hausa guda uku waxanda aka gabatar da su a tarurrukan qara wa juna ilimi da Cibiyar ta shirya, waxannan waqoqi kuwa sun haxa da waqar *Komawa Ga Allah* da waqar *Gadar Zare* ta Mudi Sipikin da kuma waqar

Kadaura Babbar Inuwa ta Aqilu Aliyu. A littafin an fexe kowace waqa bisa ma'aunin fixar waqa na ilimi waxanda suka haxa da nazarin jigo da zubi da tsarin waqa da salo da sarrafa harshe da karin waqa da dai sauransu.

Wannan littafi yana da alaqa da wannan aiki kasancewar dukkansu suna magana ne a kan wasu waqoqin Hausa kuma rubutattu, sai dai a nan za a nazarci zantuka na raha ne, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Xangambo (1979) shi ma wasu waqoqin Hausa ne ya zava ya gudanar da sharhi a kansu a inda ya fara da kawo tarihin samuwar rubutattun waqoqin Hausa tare da bayyana irin ci gaban da suka samu a tsakani na sha tara da na ashirin. Sannan kuma ya kawo wasu abubuwa muhimmai da ya kamata a ce kowace rubutacciyar waqa ta qunsa wato kamar ma'auni da qafiya da mabuxi da marufi da tsari da dai sauransu. Daga nan sai ya zavi wasu rubutattun waqoqin Hausa har guda talatin da xaya (31) daga shahararrun marubuta waqoqin Hausa kamar irin su: Shehu Xanfodiyo da Abdullahi Xanfodiyo da Nana Asma'u da Aliyu Xansidi da Aliyu Namangi da sauran makamantansu.

Akwai alaqa ta qut-da-qut tsakanin wannan aiki da wannan bincike saboda dukkansu suna magana ne a kan rubutattun waqoqin Hausa. Har wa yau kuma mawallafin ya kawo wasu waqoqin da wannan bincike zai yi nazari a kan su wato kamar waqar *Zambon Qazama* da waqar *Basukur* na Aliyu Namangi, sai kuma a nan za a nazarci raha ce a cikin su.

Har wa yau C.N.H.N (1979) an sake wallafa wani littafi mai qunshe da sharhin wasu waqoqin Hausa na wasu masana a ilimi rubutattun waqoqin Hausa. Waqoqin kuwa sun haxa da waqar *Hawainiya* da waqar *'Yanci* da kuma

Tahamisin waqar *Arewa Jamhuriya ko Mulukiya* a inda kowacce waqa aka yi mata sharhi ta yin amfani da ma'aunan nazarin waqa na zamani.

Dangantakar da ke tsakanin wannan littafi da wannan aiki ita ce dukkansu suna magana ne a kan rubutattun waqoqin Hausa, sai dai kuma a wannan binciken raha ce za a nazarta a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Diji (2004) ta wallafa littafin da ya qunshi cikakken bayani kan ma'ana da muhimmancin rubutattun waqoqin Turanci a inda aka kawo bayanai kan ma'anonin waxansu kalmomin nazarin rubutacciyar waqa a kowanne harshe ba ma a harshen Turanci kaxai ba, sannan ta bayyana yadda ake amfani da su tare da kawo nau'o'in waqoqin Turanci rubutattu, a inda aka kawo misali daga wasu waqoqin Afirka amma na Turanci, sannan aka yi sharhi taqaitacce a kansu.

Wannan aiki na Diji (2004) yana da alaqa da wannan nazari kasancewarsu dukkansu a kan rubutattun waqoqi aka gudanar, sai dai ita ta yi nazarin ne a harshen Turanci, wannan kuwa za a gudanar da shi ne a harshen Hausa, sannan kuma za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Mukhtar (2005) ya zavi wasu rubutattun waqoqin Hausa na qarni na goma sha tara da na ashirin, ya kuma nazarce su ta fuskar nahawu da qirar jumla da ke cikin kowacce waqa daga cikin waqoqi goma sha biyu da ya zava, sannan kuma ya kawo tarihin wasu fitattun marubuta waqoqin Hausa guda takwas, huxu daga ciki na qarni na goma sha tara, huxu kuma daga cikin na qarni na ashirin wato kamar irin su Abdullahi Fodiyo da Nana Asma'u da Aqilu Aliyu da Sa'adu Zungur da sauran su.

Haka kuma ya kawo ma'anar waqa da tarihin samuwarta da ire-irenta da bayanin fuskokin da masana suka dubi waqa domin nazarinta wato kamar nazarin karin waqa da amsa-amo da salon marubuci da amfani da azanci a cikin waqa, sannan kuma sai ya yi tsokaci kan arulin Hausa, wato ararrun karuruwan da akan auna rubutacciyar waqar Hausa da su wato 'Dawil, Majiid, Basiix, Waafir, kaamil, Hajaz, Rajaz, Ramal, Sariii, Hafiif, Mulari'i, da Mutaqarab.

Aikin Mukhtar (2005) na da alaqa da wannan nazari domin kuwa dukkansu suna magana ne a kan rubutacciyar waqar Hausa, sai dai a nan raha ce, za a nazarta a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

2.6.3 Muqalu

Bayan an duba kundayen bincike da bugaggun littattafai waxanda masana suka wallafa sai kuma aka waiwayi muqalu waxanda aka gabatar a game da rubutacciyar waqar Hausa, waxanda suka haxa da:

Muhammad (1980) da sa'id (1981) da Ibrahim (1982) da Muhammad (1999) da Wurma (1999) da Gusau (2001) da Auta (2001) da Mukhtar (2006) da Malumfashi (2010) sun gabatar da muqalu game da waqar Hausa, kamar yadda:

Muhammad (1980) sharhi ya yi game da alaqar da ke tsakanin marubuta waqoqin Hausa da mawaqan baka na Hausa (makaxa) ta fuskar aron karin waqa musamman wanda marubuta waqoqi kan yi amfani da su daga waqoqin baka na makaxa a inda ya warware bayani sosai tare da kawo misalai na tasirin aron karin waqa daga wasu rubutattun waqoqin Hausa guda talatin tare da kawo gindin waqoqin bakan da aka aro karin daga gare su, waxanda suka haxa da waqoqin makaxa, kamar waqoqin Caji da na Mamman Shata da waqoqin dandali, kamar

waqar *Asawwara* da waqoqin tashe ko bara kamar waqar *Allah Maimaita mana Malamai*.

Dangantakar da ke tsakanin wannan muqala da wannan aiki ita ce dukkansu suna magana ne kan rubutacciyar waqa, duk da cewa aikin nasa ya haxa da waqoqin baka amma dai duk a kan waqa suke magana, sai dai sun bambanta domin kuwa a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Sa'id (1981) ya nazarci bambancin da ke tsakanin rubutacciyar waqa da waqar baka ta Hausa, a inda ya fara da bayanin dangantakar da ke tsakanin waqar baka da rubutacciyar waqa sannan ya yi sharhi tare da kawo misalai kan muhimman abubuwan da ya kamata a yi la'akari da su yayin bambance waqar baka da rubutacciya kamar mabuxi da marufin waqa ma'auni, amsa-amo da ambaton jigon waqa da warwarar jigo da ambaton sunan mawaqi, da maqasudin yin waqa da hanyar tsara waqa, wato yadda ake yi wa waqa, da masu yin waqa da samuwar waqa da ajiye ta da sarrafa harshe, da muryar waqa da kammalar waqa da aron kalmomi.

Akwai dangantaka tsakanin wannan aiki da wannan bincike domin kuwa dukkansu suna magana ne kan rubutacciyar waqa sai dai shi ya haxa da waqar baka ta hanyar nuna bambancin da ke tsakanin waqar baka da rubutacciyar waqar Hausa a nan kuwa za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Ibrahim (1982) sharhi ya yi game da rubutattun waqoqin Hausa kafin zamanin Shehu usman Xanfodiyo a inda ya yi tsokaci kan yadda rubutattun waqoqin Hausa suka fara samuwa tun kafin zamanin Mujaddadi Shehu Xanfodiyo, sannan ya kawo tarihin wasu malamai uku da aka yi a wanxan

zamani, wato Wali Xan Masani da Malam Muhammadu na Birnin gwari da Malam Shitu Xan Abdurra'uf tare da bayanin wasu rubuce-rubucensu tare da matanin waqar Hausa guda xaya da kowannensu ya rubuta da bayanin dangantakar kowace waqa da mawallafinta.

Alaqar muqalar dai da wannan aiki ita ce duk suna magana ne a kan rubutattun waqoqin Hausa, sai dai a nan raha ce za a nazarta a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Muhammad (1999) ya gudanar da muqalarsa ce kan yadda rubutattun waqoqin Hausa suka ti tasiri kan canza xabi'u, a inda ya yi bayanin muhimmancin da rubutacciyar waqar Hausa ke da shi da yadda ta ke da tasiri kan rayuwar al'ummar Hausawa, ya kawo hujjar hakan ga irin rawar da rubutattun waqoqin Hausa suka taka tun daga lokacin jihadin jaddada addinin Musulunci a zamanin Shehu Usman Xanfodiyo wajen fahimtar da al'umma al'amuran addinin Musulunci da kyautata ibada da mu'amala da makamantansu.

Haka kuma ya yi bayanin irin rawar da rubutattun waqoqin Hausa ke takawa wajen taimaka wa hukumomi ga wayar da kan al'umma kan wasu sababbin manufofin gwamnati da sauyin yanayin rayuwa da akan samu kamar samun mulkin kan Nijeriya, tare da kawo misalai daga wasu rubutattun waqoqin Hausa na qarni na ashirin.

Akwai alaqa tsakanin wannan muqala da wannan aiki domin kuwa duk suna magana ne kan rubutacciyar waqar Hausa sai dai a nan za a nazarci raha ce, a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Wurma (1999) ya gudanar da muqalarsa kan muhimman hanyoyin nazarin rubutattun waqoqin Hausa da kuma abubuwan da suke vata rubutattun waqoqin Hausa a inda ya bayyana waqa da cewa wata aba ce da ake rerawa cikin hikima domin koyar da wasu darussa, sannan ya yi sharhi kan hanyoyin da ake bi wajen nazarin waqa rubutacciya waxanda suka haxa da sanin tarihin mawaqi da dalilin yin waqar, waxanda suka haxa da addini da ilimi da siyasa da sana'a da soyayya da sha'awa, sai jigo da warwarar jigo da zubi da tsari wanda ya qunshi ginin baiti, da yabon buxewa da amsa-amo da kari da yawan layuka da yabon kammalawa, sai salon sarrafa harshe wanda ya haxa da salon mawaqin da adon harshe, kamar tamka da kamance da alamtarwa da jirwaye da qarangiya da gwanintar harshe da aron baqin kalmomi da amfani da tsofaffin kalmomi tare da kawo misalai daga wasu rubutattun waqoqi. Daga nan kuma sai ya yi bayanin wasu abubuwa da sukan vata waqa su rage mata alkadari, waxanda suka haxa da yawan maimaita wata kalma da yawan aron baqin kalmomi da rashin amsa-amo ko daidaituwarsa da amfani da kalma a inda bai dace ba, da karyewar karin waqa.

Wannan aiki na Wurma (1999) na da alaqa da wannan nazari saboda dukkansu suna magana ne kan rubutacciyar waqa, sai dai a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Shi ma Gusau (2001) ya gabatar da qasidarsa kan sanabe-sanaben rubutu da kuma nazarin rubutattun waqoqin Hausa, a inda ya bayyana ma'anar waqa rubutatta da cewa wata aba ce wadda ake shirya maganganu daki-daki cikin azanci da nuna qwarewar harshe, sai kuma ya kawo tarihin samuwar waqa

rubutatta da bayani kan marubucin waqa da ire-iren siffofinsa da abubuwan da suka kamance shi, a inda ya bayyana mai rubuta waqa da cewa xayan mutane uku ne Jubiliyya, wato hanya ta xabi'a da ake haihuwar mutum da ita da koyo, wato ta hanyar zama da wani wanda ya iya waqa, sai kuma lalurar rayuwa ko tsananin wata buqata. Haka nan kuma mai nazarin waqa da shi ma ke da rukunoni guda uku kamar zaure/soro da almajiransu da rukunin malaman zamani da xabi'unsu, daga nan kuma sai ya yi sharhi kan dabarun da ake amfani da su wajen nazarin rubutattun waqoqi kamar gabatarwa da jigo da zubi da tsari da salo da sarrafa harshe da kammalawa wanda yakan qunshi taqaita nazari da fito da sakamako da kuma shawarwari.

Akwai dangantaka tsakanin wannan qasida da wannan aiki kasancewarsu duk suna magana kan rubutacciyar waqar Hausa, amma sun bambanta domin a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Auta (2001) ya gabatar da muqalarsa ce kan tarihin rubutattun waqoqi ne a qasar Hausa, ya fara da bayyana ma'anar waqa wadda ya ce wata manufa ce da akan bayyana a rera ta hanyar amfani da amsa-amo ko kuma rerawar ta zama ta sautin murya mai zaqi wata sa'a a haxa da kixa da sauran salon jin daxi ga mai sauraro, domin jawo hankalinsa ga kuma manufa, kuma ta bambanta da maganar baka ta yau da kullum da zube da wasan kwaikwayo, sannan sai ya yi bayanin ire-iren bambancin sigogi da ke akwai a tsakanin waqar baka da rubutacciyar waqa ta fuskar aiwatarwa da zubi da tsari da halayyar lokaci wato kamar daidaituwar kalmomi da tsarin kari da amsa-amo a rubutacciyar waqa da muhimmancin kixa da zaqin murya da aiwatarwa cikin qugiya a waqar baka, sannan sai ya shiga

bayanin tarihin samuwar rubutattun waqoqin Hausa tun daga lokacin da ya gabaci zuwan Musulunci har zuwa qarni na ashirin tare da yin sharhi kan jigogin waqoqin a lokutansu mabambanta.

A muqalar Auta (2001) tana da alaqa da wannan bincike domin kuwa duk suna magana ne kan rubutattun waqoqin Hausa a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Yayin da Mukhtar (2006) ya gabatar da muqalarsa kan irin gudummuwar da rubutattun waqoqin Hausa suka bayar wajen addaba tarihin siyasar Nijeriya, a inda ya bayyana ma'anar waqa da cewa wani saqo ne a cikin furuci da kuma lafazi mai azanci wanda ake gabatar da shi ta hanyar daidaitattun kalmomi masu tsari da kuma qa'ida da sauran dabaru masu sa jawo hankali, ya ce saboda haka ita dai waqa maganar hikima ce da nuna fasaha, sai kuma ya bayyana yanayin wanda ya ce lallai ne a sami rerawa da hawa da sauka na murya mai daxi, sannan da hikima da fasaha a cikin daidaitattun kalmomi masu daidaitaccen tsari da amsa-amo a waqa rubutatta, sai kuma salo da zubi da tsari. A waqar baka kuma akan samu kixa da amshi sannan sai ya yi nazarin gudummuwar da rubutattun waqoqin Hausa ke bayarwa wajen adana tarihin siyasar Nijeriya cikin waqoqinsu, tun daga qarni na goma sha tara har ya zuwa yanzu, kamar waqoqin siyasar Musulunci a zamanin Shehu Usman Xanfodiyo da waqoqin Jam'iyyun siyasa a Jamhuriya ta biyu da ta uku.

Wannan nazari na Mukhtar (2006) yana da alaqa da wannan aiki kasancewarsu duk suna magana kan rubutacciyar waqa, sai dai sun bambanta domin a nan za a nazarci raha ce a wasu waqoqin Aliyu Namangi.

Malumfashi (2010) Wa'azi ya nazarta a rubutattun waqoqin Hausa na qarni na ashirin inda ya qalubalanci ra'ayin masu cewa waqoqin qarni na ashirin jigonsu na sha'anonin duniya ne ba na addini ba ne, ya fara da bayanin waqar da akan xauka cewa ita ce kadarko tsakanin waqoqin qarni na sha tara da na ashirin dangane da shekarar da aka wallafa ta, wato waqar *Tabarqoqo* ta sarkin Zazzau Aliyu xan Sidi, ya nuna cewa ba ita ya kamata ta zamo waqar farko a qarni na ashirin ba waqar *Zuwan Annasara* ta sarkin Musulmi Attahiru ce ta kamata ta zamo waqar farko, sa'annan kuma ya bi wasu muhimman jigogin waqoqin qarni na ashirin da ake lissafa su a matsayin baduniyai, kamar waqoqin siyasa na murnar samun 'yancin kai na yaqin basasa da waqoqin yabo, ya nuna cewa akwai ruhin addini a cikinsu kuma a kansa aka gina su yana mai kawo misalai daga waqoqin Marubuta daban-daban kamar Aliyu Namangi da Sa'adu Zungur da Bello Gixaxawa da Aqilu Aliyu da gambo Hawaja da sauransu.

Har wa yau kuma ya nuna cewa wasu daga jigogin waqoqin qarni na ashirin da ake wa kallon na duniya ne, kamar waqoqin yabon mutanen qwarai, suna da takwarori a waqoqin qarni na sha tara.

Wannan aiki na Malumfashi (2010) yana da alaqa ta kusa da wannan bincike domin kuwa duk suna magana ne a kan rubutattun waqoqin Hausa, sannan kuma ya kawo misali da waqar *Basukur* ta Aliyu Namangi, wanda ta na xaya daga cikin waqoqin da za a nazarta a wannan aiki domin a fito da zantuka na raha daga cikinsu.

2.7 Naxewa

Wannan babi ya kammala bayanan gudanar da waiwaye kan ayyukan da suka gabata, ayyukan da masana da manazarta suka gudanar waxanda suka shafi raha da wasu ayyuka kan Aliyu Namangi da kuma waxanda suka shafi rubutattun waqoqin Hausa masu dangantaka ta kusa da ta nesa da wannan aiki, wato tun daga kan kundayen bincike na digiri na xaya da na biyu da na uku, sai muqalu da kuma bugaggun littattafai.

Amma duk da haka waiwayen da nazarce-nazarcen da aka yi a kan raha ba su wuce cikin cokali ba musamman ma game da raha a waqoqin Hausa kasancewar manazartan da suka gudanar da nazari kan raha sun fi mayar da hankali ga wasan kwaikwayo da qagaggun labarai na raha, wanda hakan na xaya daga cikin dalilan gudanar da wannan bincike. Haka kuma binciken da aka yi kan ayyukan da aka gudanar kan Aliyu Namangi su ma ba su taka kara sun karya ba, sakamakon qarancin bincike dangane da rayuwa ko gudummuwar wannan marubuci wato Aliyu Namangi sai dai kuma a kullum ana samun qaruwar ire-iren waxannan ayyuka wanda ana sa ran nan gaba su fi kowanne aiki yawa musamman a fagen rubutattun waqoqin Hausa.

BABI NA UKU

HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

3.0 Gabatarwa

Kowane irin bincike musamman ma a wannan fage na ilimi ba zai gudanu ba sai an bi wasu hanyoyi domin samo bayanai gamsassu domin aikin ya inganta. Wannan ya sa ake ziyartar wasu manyan masana ko wasu muhimman wurare domin tattaro ire-iren waxannan bayanai domin gudanar da bincike. Hakan zai taimaka matuqa wajen kaiwa ga nasarar kowane irin bincike.

Saboda haka, a wannan babi an yi bayanin hanyoyin da aka bi wajen tattaro bayanai da suka taimaka domin gudanar da wannan bincike. Wasu bayanan an samo su kai tsaye ta hanyar tattaunawa da wasu manyan malamai waxanda suka gudanar da bincike dangane da wasu waqoqin Aliyu Namangi. Wasu bayanan kuwa an samo su ne a wasu xakunan karatu na wasu jami'o'i ta hanyar nazartar kundayen bincike da wasu littattafai da muqalu waxanda malamai da manazarta suka gabatar. Har wa yau kuma an samo wasu bayanan ne ta hanyar ziyartar wasu kafafen yaxa labarai, musamman ma wajen samo waqoqin da binciken ya gudana a kansu.

3.1 Xakunan Karatu

Domin cim ma burin wannan bincike an ziyarci wasu xakunan karatu a Jami'o'i daban-daban, wato kamar xakin karatu na Sashen Koyar da Harsunan Najeriya, Jami'ar Usman Xanfodiyo, Sakkwato, da xakin karatu na Sashen Harsunan Najeriya da Al'adun Afirka na Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya da xakin karatu na Sashen Koyar da Harsuna da Kimiyya, Jami'ar Bayero Kano da xakin karatu na Sashen Hausa na Kwalejin Ilimi da ke

Zariya. A nan ne aka duba kundayen bincike, da wasu littattafai, da muqalu waxanda suka yi magana dangane da abubuwan da suka shafi rubutacciyar waqa da raha. Sai kuma waxanda suka yi magana game da rayuwa da ire-iren ayyukan da Aliyu Namangi ya gudanar a lokacin rayuwarsa.

3.2 Ziyara

Ziyara wata aba ce muhimmiya ga duk wani mai gudanar da bincike domin a nan ne za a ga abubuwa quru-quru , saboda gani ya kori ji. Domin haka, an ziyarci wasu gidajen rediyo domin samo wasu bayanai da za su taimaka wajen gudanar da wannan bincike. An kai ziyara gidan rediyon tarayya na Kaduna (F.R.C.N) a inda aka samo wasu bayanai da kuma waxannan waqoqi da aka nazarta. Haka kuma an ziyarci gidan rediyo na Jihar kaduna da gidan rediyo na Queens Fm da ke Zariya da gidan rediyo na Nagarta da ke marabar Jos, Kaduna. Har wa yau kuma an ziyarci taskar tattalin fasahar baka (O.D.U) da ke Sashen Harsunan Najeriya da Al'adun Afirka, Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya. A inda aka samo wata hira da ta gudana a tsakanin Aliyu Namangi da Farfesa Xalhatu Muhammad da Dakta Magaji Tsoho Yakawada.

3.3 Ganawa

Wannan ma wata hanya ce da akan bi wajen gudanar da bincike, saboda kusan wajibi ne ga duk wani mai gudanar da bincike da ya samu ganawa da mawallafin da ake gudanar da binciken a kansa idan yana raye. Ko kuma a samu ganawa da wasu manyan malamai ko kuma waxanda suka yi rayuwa tare da shi idan ya shuxe.

Saboda haka, wannan bincike ya samu ganawa da wasu mutane waxanda suka rayu tare da Aliyu namangi, domin qara samun bayanai na zahiri kuma ingantattu.

Waxannan mutane sun haxa da Mal. Umar na Balarabe (malamin mata) da Mal. Murtala Aliyu Namangi

3.3.1 Hira da Malam Umar

An yi hira da malam Umar ta hanyar tambaya yana bayar da amsa a ranar Alhamis 8/4/2012 kamar haka:

- Allah ya gafarta malam ya sunanka?

  Sunana Malam Umar na Malam Balarabe, amma an fi sani na da malamin mata.

- Wani dalili ne ya sa ake kiranka da malamin mata?

  Saboda a baya mata kawai nake koyarwa, kafin daga bisani matata ta koma tana koyar da matan, ni kuma na koma ina koyar da maza a zaure.

- Malam ko mece ce alaqarka da Aliyu Namangi?

  To! Babbar magana a taqaice dai mu aminan juna ne, kuma ina xaya daga cikin sakatarorin Aliyu Namangi, wato masu yi masa rubutu, kasancewar ba ya gani da idanuwansa.

- Malam Umaru ko mene ne dalilin da ya sa Aliyu Namangi ya wallafa waqar qazama?

  Aliyu Namangi ya wallafa waqar qazama, wato akwai wata rana muna zaune a majalisin Aliyu Namangi muna hira, sai wani malam Isa ya ce "Malam Aliyu ya kamata ka wallafa waqa ga ire-iren matan nan qazamai ko sa bar yin qazanta". Aliyu Namangi ya amsa masa kuma ya wallafa, ya kuma sanya mata suna waqar *Zambon Qazama*.

- To Malam Ummaru ka ce kana xaya daga cikin sakatarorin Aliyu Namangi, kana nufin akwai wasu ke nan?

  E! akwai malam Xalhatu da ke Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya da kuma malam Magaji Tsoho Yakawada shi ma yana Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya da kuma malam Amadu, shi ban san inda yake ba a yanzu.

- Malam Ummaru Aliyu Namangi ya ambaci wasu mutane a wasu waqoqinsa ta hanyar yi musu ba'a, ko ka san waxannan mutanen?

  Qwarai kuwa duk 'yan uwansa ne na jini kuma akwai wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu. Saboda haka ba wani abu ba ne, wasa ne kawai irin na abokan wasa.

3.3.2 Hira Da Murtala Namangi

An yi hira da Alhaji Murtala Namangi ta hanyar tambaya yana bayar da amsa a ranar litini 12/4/2012.:

- Malam ya sunanka?
  Suna na Alhaji Murtala Aliyu Namangi.

- Malam shekarunka nawa?
  Shekaruna arba'in da shida.
- Mece ce dangantakarka da Aliyu Namangi?
  Mahaifina ne, ni ne xansa na tara, kuma mahaifiyata ita ce matarsa ta biyu.
- Mene ne sunan mahaifiyarka?
  Sunanta Zainab, kuma Allah ya yi mata rasuwa, Allah ya jiqanta, amin.
- Malam Murtala kaima kakan wallafa waqoqi ne kamar mahaifinka?
  A'a, ni ban iya wallafa waqa ba, ko rera wa ban iya ba, sai dai akwai wasu waqoqin marigayi da nake yawan sauraron su.
- Kamar wacce waqa da wacce waqa?

Kamar waqar *Imfiraji* da waqar *Tsarabar Madina*

- Malam Murtala ku nawa ne ‘ya’yan Aliyu Namangi?
  Mu sittin da huxu ne (64). Amma ya rasu ya bar mu, mu ashirin da xaya (21): maza goma sha huxu (14) mata bakwai (7).
  Allah ya jiqan malam Aliyu Namangi, amin.

3.4 Ra’in Bincike

Wannan bincike ya dogara ne ga ra’in isar da saqo (dialogical theory) domin yin nazarin raha a wasu waqoqin Aliyu Namangi. Shi dai ra’in isar da saqo ra’i ne wanda wani masanin ra’o’in adabi mai suna Michail Balchtin xan qasar Russia ya qirqiro a cikin littafin *Cultural Criticism A Premier of Key Concepts* na Arthur Asa Berger (1995).

A cikin wannan littafi ne Bakhlin ya yi da’awar cewa magana ko rubutu na tattare ne da wani saqo da ake son a isar ga al’umma. Haka kuma, rubutun na ko maganar nan suna qunshe ne da abin da aka faxa ko aka rubuta saqo ne ga jama’a da kuma irin sakamakon da za su samu bayan sun karanta ko saurara.

Ra’in isar da saqo ra’i ne da ke nuna cewa idan mutum ya yi magana ko ya yi wani rubutu to dole akwai wata manufa ta yin wannan maganar ko rubutun.

Saboda haka, an zavi wannan ra’i ne domin a xora wannan bincike a kai kasancewar yadda binciken ya gudana kan raha, ita kuwa raha ana aiwatar da ita ce domin wata manufa. Haka kuma raha na haifar da nishaxi da bayar da dariya ga kuma qara danqon zumunci a tsakanin dangi ko abokan zama ko na sana’a.

Wannan ya sanya mawaqa da dama yin qoqari wajen yaxa manufofi ko wa’azi ko gargaxi ta hanyar amfani da zantuttuka na raha domin samun damar isar da saqon da ke qunshe a waqoqinsu cikin sauqi. Domin haka, waxannan waqoqi da aka nazarta a wannan

aiki, waqoqi ne da Aliyu Namangi ya wallafa su da nufin wa'azi, ya kuma isar da saqon da ke qunshe a waqoqin cikin raha da nishaxi.

3.5 Kammalawa

An kammala wannan babi bayan an kawo bayanai dangane da hanyoyin da aka bi wajen tattaro bayanai da suka taimaka wajen gudanar da wannan bincike. Kamar dai yadda aka bayyana, an yi hira da wasu mutane waxanda suka yi rayuwa da Aliyu namangi domin jin ta bakinsu game da rayuwa da kuma wasu ayyukan Aliyu Namangi.

A taqaice dai an bi hanyoyi daban-daban domin tattaro muhimman bayanai waxanda suka kai ga wannan aikin tudun mun tsira.

BABI NA HUXU

RAHA A WASU WAQOQIN ALIYU NAMANGI

4.0 Gabatarwa

Wannan babi ya qunshi bayani ne dangane da yadda Aliyu Namangi ya sarrafa raha a wasu waqoqinsa, tare da yin tsokaci game da ire-iren nau'o'in rahar da aka sarrafa a waxannan waqoqi.

Aliyu Namangi ya sarrafa nau'o'i biyu na raha a waxannan waqoqi, wato raha barkwai da raha shaguvau. Ya sarrafa raha barkwai ne domin ya qarfafa danqon zumunci da ke a tsakaninsa da 'yanuwansa. A yayin da ya sarrafa raha shaguvau domin yin suka ga wasu munanan xabi'u da Allah (SWT) ya yi hani da a aikata su.

Saboda haka, wannan babi yana tattare ne da bayanai game da yadda Aliyu Namangi ya sarrafa ire-iren nau'o'in raha a wasu waqoqinsa.

4.1 Raha Barkwai A wasu Waqoqin Aliyu Namangi

Raha barkwai wasu zantuttuka ne na bayar da dariya da Allah (S.W.T) ya hore wa wasu mutane iya magana ke gudanarwa a tsakanin al'umma domin su nishaxantar da jama'a. haka kuma wasa ne da akan zaqe wajen qoqarin ganin cewa an cusa nishaxi ko bayar da dariya ko da kuwa zai kai ga an karya wasu

qa'idojin zamantakewar al'ummar Hausawa. Wato kamar batsa ko bugu da jefefeniya ko hamvari a tsakanin masu gudanar da wasan. (Aminu 2012:48).

Har wa yau kuma akan bayar da wasu 'yan gajerun labarai da suka tava faruwa ko aka qirqira da nufin daxaxawa ko tsokana tsakanin dangi. Haka kuma raha barkwai wasa ne na dangantaka da al'ada ta yadda da wanzuwarsa a tsakanin mutane biyu ko a tsakanin al'umma. Domin a duk lokacin da abokan wasa suka haxu sai sunzolayi juna ko su tunzura juna, amma ba tare da an samu wani savani ba. (Brown, 1952:33-34).

A dunqule a iya cewa raha barkwai wasu zantuttuka ne masu bayar da dariya da nishaxi a tsakanin al'umma da suka aminta da wanzuwar wasan domin adana tarihinsu da kuma yauqaqa zumunci.

Al'ummar Hausawa sun aminta da wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu dimin qarfafa zumunci da ke a tsakaninsu. Wannan ce damar da Aliyu Namangi ya samu wajen ambaton sunayen wasu mutane a fili cikin wasu waqoqinsa ba tare da ya sakaya sunayensu ba.

Har wa yau kuma Aliyu Namangi ya siffanta ko danganta waxannan mutane da wasu abubuwa daban-daban ba domin komai ba sai don ya samar da nishaxi a kuma yi musu dariya. Wato kamar yadda ya bayyana irin taqaddamar da ta kasance a tsakanin keke (Basukur) da malam Sale, a waqar *Basukur*,

Ga yadda yake cewa a waqar:

Sukai qadda da Sale a kan kadarko,
Sai yace "Haba Sale ba zan yada kai ba.

Garin suka wantsala haka, kan yi qwace,
Ashe ba Sale ne a cikin ruwa ba?

Ya bi shi ya bangaje, ya buge yana ce,
"A zo a gani, izan ban yada kai ba.

Malam Sale sai da ya tuve riga,
Ya sa a ka ga Sale har bai sha ruwa ba,

Ya tashi ya hau tudu, keke ya bi shi,
Da rigar Sale keke bai sako ba.

Su Malam Sanda duk suka tar ma keke,
Da ban magana, ya ce "Ba zai sako ba.

Ya ma rantse da jirgi har da mota,
Wai ba za shi sako izan ba a sa wuqa ba.
(Yakawada, 1987:326)

A nan duk waxannan zantuttuka da Aliyu Namangi ya ambata cewa sun faru a tsakanin Malam Sale da keke raha ce kawai. Saboda babu wata taqaddama da ta faru a tsakaninsu. Hasali ma taqaddamar ta faru ne a tsakanin shi kansa Aliyu Namangi da keken a lokacin da ya je taron suna a qauyen Yakaji. Saboda haka sai ya danganta wannan taqaddamar da cewa ta faru ne a tsakanin malam Sale da keke ta hanyar yi masa ba'a domin a yi dariya. Kamar inda ya nuna cewa keken ya kama rigar malam Sale ya riqe a inda 'yan uwansa suka roqi keken da ya sakar wa malam Sale riga amma ya ce "Ba zai saka ba". Ya ci gaba da cewa "Ya ma rantse da jirgi da mota ba zai sakarwa malam Sale riga ba, sai dai a yanke rigar da wuqa".

Waxannan duk zantuttuka ne na raha da bayar da dariya saboda yadda aka nuna wai keke ne zai riqe wa wani riga har ma ana roqonsa da ya sakar masa riga amma ya qi. Har ma yana rantsuwa da jirgi da mota ba zai saka ba.

Haka kuma idan aka dubi inda mawaqin ya mutuntar da keken inda ya nuna cewa sun zanta da malam Sale. Har ma keken ya ce: "Ba zai kayar da shi

ba" wato kamar inda ya ce "Haba Sale ba zan ya da kai ba". Sannan kuma bayan ya kayar da shi sai yake cewa "A zo a gani izan ban yada kai ba".

Waxannan zantuttuka duk raha ce kawai, saboda babu wanda ya tava jin cewa keke ya yi magana. Amma a nan sai aka nuna hakan har ma yana yi wa abokin maganarsa gwalo inda ya ce "A zo a gani izan ban yada kai ba". Wannan raha ce kawai domin a samar da nishaxi da kuma ban dariya.

Har wa yau kuma Aliyu Namangi ya yi irin wannan ba'ar ga malam Sanda wanda qani ne ga malam Sale. Kuma yana xaya daga cikin mutanen da Aliyu Namangi ya nuna cewa sun roqi keke da ya sakar wa xan uwansa riga amma ya ce "Ba zai saka ba". Saboda haka shi ma Aliyu Namangi bai qyale shi ba. Domin shi ma ya ambace shi da cewa shi ma irin wannan taqaddama ta faru a tsakaninsa da keke. Ga yadda ya faxa a waqa:

Malam Sanda sun shirya da keke,
Wai yana qaunar sa ba domin tsiya ba.

Ya ce "Haba! Malami babba kamarka?
Ba zan iya yada babban malami ba.

Izan dai za ka hau ni, ka tara riga,
Da wando, ba ka hau ni hawan isa ba.

Ya tashi hawa ashe bai tattara ba,
Ya fizgo malamin ba a jinjina ba.

Ya yasai nan da nan a tsakar gidansa,
Cikin matansa tun ba a kai daxe ba.

Ya ce "Bari nai kuren yashe ka, malam,
Zama ban kai ka bakin kasuwa ba.

Ban na san in yada mutum na kirki,
Izan ba inda za a yi dariya ba.

Da motsa qararrawarka da kama burki,
Ba za su hana ni in jefad da kai ba.

Ya ce "To, ba ni qara hawan ka keke,
Ya ce masa "Ko a dankiya ba kula ba".

Hawan da rashin hawan a gare ni xai na,
Ban ga abin da zai cutad da ni ba.
(Yakawada,1987: 326).

Haqiqa waxannan zantuttuka da Aliyu Namangi ya ambata cewa sun faru duk raha ce kawai. Domin kamar yadda aka ambata a baya cewa babu wata taqaddama da ta faru a tsakanin malam Sale da keke. Haka ma babu wani abu da ya faru a tsakanin malam Sanda da keken. Ba'a kawai yake musu domin a yi musu dariya kasancewarsu na abokan wasansa. Kamar inda ya nuna cewa malam Sale ya hau keke ba tare da tattara rigarsa da wandonsa ba. Saboda haka keken ya fizgo shi ya kayar da shi kuma a gaban matansa. Duk wanda ya ji wannan ya san raha ce kuma abin dariya ne a ce babban mutum ya faxo a keke kuma a gaban iyalansa. Sannan kuma bayan ya faxo sai keken ke cewa ai ma shi kuskure ya yi da ya kayar da shi a cikin gidansa ba a bakin kasuwa ba inda za a yi masa dariya domin wai shi ba ya kayar da mutanen kirki sai a inda za a yi musu dariya. Waxannan duk zantuttuka ne na raha ya yi wa malam Sanda ba'a domin a yi masa dariya.

Wani abin dariya kuma shi ne inda ya nuna cewa keke ya gindaya wa malam Sanda wasu sharuxa kafin ya hau shi. Amma tun da ya kasa kiyaye waxannan sharuxa to fa ko da ya kaxa qararrawa ya kuma kama burki to babu abin da zai hana bai kayar da shi ba in ji keken. Saboda ya yi watsi da sharuxan da

ya gindaya masa. Waxannan duk zantuka ne na raha saboda babu yadda za a yi a ce wai keke ne ke furta waxannan zantuttuka har ma yana bayar da wasu sharuxa ga mahayinsa. Kuma ma wai har yana magana da harshen Ingilishi inda yake cewa “Ko a donkiya” (wai shi bai damu ba).

Tabbas duk wanda ya ji cewa keke ne ke faxar waxannan maganganu babu abin da zai hana shi dariya domin ya san raha ce kawai a ce keke na faxan waxannan maganganu. Wannan ke qara tabbatar da cewa Aliyu Namangi ya ambaci waxannan mutane ta hanyar yi musu ba’a a kuma yi musu dariya a matsayinsu na abokan wasansa na jini.

Wato kamar yadda ya gabata a baya cewa babu wata taqaddama da ta faru a tsakanin waxannan mutane da keke. Amma taqaddamar ta faru a tsakanin keken da Aliyu Namangi a lokacin da ya tafi taron suna a qauyen Yakaji xaya daga cikin qauyukan Dabai a inda wani yaro ya goya Aliyu Namangi a keke domin zuwa wata unguwa a kan hanyarsu ta dawowa keken ya yi faci. Bayan an gyara suna cikin tafiya kuma kan keken ya kwance suka wantsala suka faxa ruwa kacar keken ta kama rigar Aliyu Namangi sai da aka yanke rigar da wuqa. Sannan kuma suka rasa sallar Juma’a a dalilin waxannan matsaloli da suka faru.

Bayan sun dawo gida sai yaron ya zo ya ce wa Aliyu Namangi ya kawo sule da sisi kuxin hayan keken da suka hau. Haka nan ya xauka ya bayar ba tare da an rage masa ko kwabo ba. Da Aliyu Namangi ya dawo gida Zariya kuma a dai-dai lokacin da aka buqaci mawaqa na baka da marubuta waqoqin Hausa da su shirya waqoqi domin nuna murnarsu na samun ‘yancin Arewacin Nijeriya.

Domin haka da ya tashi shirya waqar Basukur sai ya yi amfani da wannan dama ya danganta duk matsalolin da ya haxu da su a sanadiyyar hawa keken ga waxannan mutane wato malam Sale da malam Sanda. Saboda akwai wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu da Aliyu Namangi[1].

Haka kuma Aliyu Namangi ya yi irin wannan ba'ar ga wasu mata waxanda akwai irin wannan wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu. Wato Gude da Kumatu da kum[2]a Ta-sallah.

Mawaqin ya ambaci Gude a wasu waqoqinsa ta hanyar yi mata ba'a da wasu sunaye ko wasu xabi'u daban-daban. Kamar inda ya nuna cewa Gude haxamammiya ce, kuma ba ta iya girki ba, sannan kuma ba ta qoshi, kuma tana da irin xabi'ar nan ta wasu mata masu tsame naman miya su cinye. Idan maigidanta ya tambeye ta ina naman da ya kawo? Sai ta ce masa ai duk kitse ne saboda haka ya narke a miya. Ga yadda ya faxa a waqar.

Gude ba qoqari ba, ga kasa girki,
Ga haxama a zuci, qoshinta fama.

Ran girkinki ba a qoshi da gixi,
Shi naman miyan ki cinye a tsama.

In ta ga ka fito kamar za ka zaure,
Sai sababi ya tashi don vata girma.

Bar neman fita, ina tsame nama,
Yau dai kai rabon a zage ka kai ma.

Tun da ka sai kitse, ya narke a girki,

[1] (Hira da Malam Umar Na Mal. Balarabe Malamin Mata Kusfa Zariya. Sakataren Aliyu Namangi ranar Alhamis, 8/4/2012).

In aka zo rabo, rabonsa fama,

Wanda ka ba shi qanqani, sai ya raina,
Kowa so shike ya karva da dama.

Rannan ma ka sai qashi na ci zagi,
Gun qwarin gidanka mai ya da girma.
(Yakawada, 1987: 323-324).

Waxannan duk zantuttuka ne na raha da Aliyu Namangi ya yi wa Gude ba'a da su domin a yi mata dariya. Saboda duk matar da aka ambata a matsayin haxamammiya kuma ba ta qoshi, sannan kuma ga ta varauniya mai tsame nama a miya. Idan an tambaye ta sai ta ce ai duk kitse ne ya narke a miya.

Sannan kuma idan mijinta ya ganta lokacin da ta ke tsamar naman sai ta kama sababi tana zaginsa. Haqiqa duk matar da aka danganta ta da waxannan xabi'u ta zama abar dariya.

Saboda haka waxannan zantuttuka da Aliyu Namangi ya ambata game da Gude ba halayenta ba ne, ba'a ce kawai yake yi mata domin a yi dariya. Dalili kuwa shi ne ya bayyana sunanta a fili ba tare da ya sakaya ba. Haka kuma ba ya yi haka ba ne da nufin muzantawa ko cin fuskar Gude ba.

Ba'a kawai irin tasu ta abokan wasa domin ya qara qarfafa zumuncin da ke tsakaninsu, saboda ita ma Guden sai da ta rama wannan ba'ar da Aliyu Namangi ya yi mata.

Domin bayan da Gude ta ji ire-iren abubuwan da ya ambace ta da su a waqarsa ta tafi gidan Aliyu Namangi ta same shi ta yi masa tsiya domin ta rama ba'ar da ya yi mata.

Amma kuma duk da haka Aliyu Namangi bai qyale ta ba domin ya qara ambatonta a wata waqar inda ya yi mata ba'a da cewa ta tambayi mijinta kuxin

kitso ya hana ta. Sannan kuma ya kira ta da mara hankali domin ga sha'ani a gabansa ga kuxin gishiri da daddawa duk a kansa sannan kuma ta tambaye shi kuxin kitso. Ga yadda ya faxa a waqar.

Ai na san ba ki da hankali,
Domin ki in bar sha'ani na.

Gishiri, dadawa, da kuxin awo,
Duk sai in fitar a jakana,

Ka na in ba ki kuxin kitso,
Ga cin ki da sha a jikina.

Da gamo da abokanni ka ce,
Yau na so dukan matana.

Ka san Gude ba ta da hankali,
Ita ke neman tono na.

Wai sai in ba ta kuxin kitso,
Ga buki a gidan surukai na.
(Yakawada, 1987: 309).

Aliyu Namangi ya wallafa wannan waqa ce da nufin wa'azi ga wasu maza da ba sa kula da buqatun matansu sai dai sun gwammace da su kashe kuxinsu ga makaxa da maroqa. Saboda haka sai ya danganta Gude da cewa tana xaya daga cikin matan da mazansu ke da irin wannan xabi'a maras kyau. Amma kuma duk ba'a ce yake yi wa Gude cikin raha domin a yi mata dariya.

Wani abin ban dariya a waqar shi ne inda ya nuna mijin Gude yana faxa a kan kuxin kitso. Har ya na yi mata gori da cewa shi ke sayen daddawa da gishiri. Sannan kuma ga awo duk shi yake yi kuma ta tambaye shi kuxin kitso.

Saboda haka wannan duk ba'a ce kawai yake yi wa Gude domin mijin Gude mutumin kirki ne, kuma na'ibin limamin qauyensu. Wannan ya qara tabbatar da cewa Aliyu Namangi ba'a ce yake yi wa Gude kuma a yi dariya.

Haka kuma Aliyu Namangi ya ambaci Kumatu ta hanyar yi mata ba'a da cewa Kumatu qazamar mace ce. Kumatu qanwa ce ga Gude, saboda haka ita ma ta zama abokiyar wasansa. Wannan ya sa ya ambace ta a waqarsa domin yi mata ba'a. ga yadda ya faxa a waqar.

In ta ce da ni qazama in rama,
Wanda ya san Kumatu ya san qazama.
(Yakawada, 1987:324)

Aliyu Namangi ya ambaci Kumatu da qazama a matsayin ramuwa domin lokacin da Gude ta je gidansa tana yi masa faxa ta kira shi da qazami. Saboda haka ya ce "In ta ce da ni qazama in rama "wanda ya san Kumatu ya san qazama".

Wannan duk ba'a ce kawai yake yi wa Kumatu domin ba qazamiyar mace ba ce. Ya ambace ta ne kawai domin raha kuma a yi dariya.

Har wa yau kuma ya ambaci Ta-sallah wanda ita ma qanwa ce ga Gude da Kumatu saboda haka ita ma tana matsayin abokiyar wasansa na jini. Saboda haka ya yi mata ba 'a da abubuwa daban-daban a waqarsa kamar inda ya ambace ta da haxamammiya ga cin tsiya sannan kuma ba ta qoshi. Ga yadda ya faxa a waqar:

In ta ce ina da ci in rama,
Domin ga Ta-sallahj qoshin ta fama.

Kwana goma jere, haifarta goma,
Ba taran miji ga haifar qazama.

Ko bante ta qetare, sai ta haihu,
In ka san kuxi su qare a suna.
(Yakawada, 1987: 324).

Haqiqa waxannan zantuttuka duk raha ce kawai Aliyu Namangi ya yi amfani da ita ta hanyar yi wa Ta-sallah ba'a domin a samu nishaxi a kuma yi dariya. Saboda duk inda aka ce ga wata mace qazama kuma kwana goma a jere

kullum sai ta haihu, sannan kuma mijinta ba ya kusantarta saboda qazantarta kuma ba ta qoshi ga cin tsiya. Tabbas duk wanda ya ji wannan zancen ya san raha ce kawai kuma abin dariya ne a ce an samu mace da waxannan abubuwa.

Saboda haka wannan raha ce kawai Aliyu Namangi yake yi wa Ta-sallah ba'a domin a yi dariya saboda tasirin wasan zumunta na dangi da ke tsakaninsu. Wannan ce damar da Aliyu Namangi ya samu har ya ambaci sunayensu ta hanyar danganta su da abubuwa iri-iri ba tare da ya sakaya sunayensu ba.

Haka kuma su ma waxannan mutanen da Aliyu Namangi ya ambata a waxannan waqoqin nasa, sannan kuma ya danganta su da wasu xabi'un da ba nasu ba. Babu wani abu da zai dame su domin sun san cewa duk raha ce kawai saboda dangantakar da ke tsakaninsu. Sai dai kawai su ma za su rama irin wannan ba'ar da ya yi musu. Wato kamar yadda Gude ta kasa jurewa lokacin da ya yi mata ba'a a waqar zambon qazama. Domin ta tafi har gida ta sami Aliyu Namangi ta yi masa tsiya irin tasu ta abokan wasa a matsayin ba'ar da ya yi mata.[3]

4.2 Raha Faxi-in-Faxa A Wasu Waqoqin Aliyu Namangi

Faxi-in-faxa wata hanya ce ta samar da raha da nishaxi a tsakanin al'ummar Hausawa musamman ma ga waxanda akwai dangantaka da ka iya haifar da wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu. Faxi-in-faxa kan wakana ne a tsakanin vangarori biyu na mutane ta hanyar amfani da wasu zantuttuka na raha domin a samar da nishaxi da ban dariya.

Saboda haka, faxi-in-faxa wata hanya ce ta gudanar da wasu zantuttuka cikin raha domin a samar da nishaxi a kuma yi dariya a tsakanin vangarori biyu na

[2] (Hira da Malam Umar na Mal. Balarabe (Malamin mata) Kusfa Zariya. Sakataren Aliyu Namangi Ranar Alhamis 8/4/2012)

masu magana. Wani lokaci kuma akan mutuntar (personification) da dabbobi ko wani abu mara motsi a rinqa zantawa da shi domin a yi dariya da nishaxi.

Wato kamar yadda Aliyu Namangi ya mutuntar da keke (Basukur) har aka samu faxi-in-faxa a tsakanin keken da wasu mutane. Wannan mutuntarwar keken ya bai wa Aliyu Namangi nasarar samar da raha da nishaxi a waqar. Ga yadda wannan zantawar ta kasance tsakanin keken da waxannan mutane.

Na ce masa "Basukur riqa sawwaqewa"
Ya ce "Malam, hala ba ka sanni ne ba".

Ina da tsiya biyar: farkonsu fanca,
Nakan buga bindiga ba mai wuta ba,

Im vavvake zuciya in faxi da sawu,
Cikin daji kamar ba a je da ni ba,

Muna tafiya nakan kuma fizge kai na,
Muka faxa kwazazzabo, ni ban kula ba.

Ina da ciki ana ce mai kurumbo,
Karambanin hawa ba ka saya ba,

Hanjina kaca mai kama riga
Mu fizgo mai hawa ni ban kula ba

Tsiya na can mu je bisa kan kadarko,
Maxaixaici, in ce ba za mu hau ba.

In hau bisa kafaxar mahayi in zauna,
Kamar mahayin da xai bai hau ni shi ba.
(Yakawada, 1987: 325).

Wannan ce zantawar da ta kasance a tsakanin keke (Basukur) da Aliyu Namangi. A inda aka yi amfani da wasu zantuttuka na raha domin samar da nishaxi da kuma ban dariya. Domin kowa ya san keke ba mutum ba ne kuma ba ya motsi. Amma an mutuntar da shi yana magana tamkar xan Adam. Har yana bayyana ire-iren tsiyarsa kamar faci wato tayar keken takan fashe idan ana tafiya.

Sannan kuma idan ana tafiya keken yakan qwace ya faxa kwazazzabo. Haka kuma yana da ciki ana ce masa kurumbo saboda haka duk wanda ya hau keken ba kurumbo to ya yi karambani. Domin kacar keken za ta kama masa riga ta fizgo shi ya faxo qasa.

Duk waxannan zantuttuka wai keke ne yake faxa wa Aliyu Namangi saboda ya nemi da ya yi masa ragi na kuxin hayan keken. Haqiqa duk wannan raha ce kawai ya yi amfani da ita domin ya samar da nishaci a kuma yi dariya. Saboda keke ba mutum ba ne kuma ba ya motsi sai an motsa shi. Haka kuma duk wanda ya ji ire-iren zantuttukan da aka yi amfani da su a zantawar babu abin da zai hana shi ya yi dariya. Kamar inda keken yake cewa “Imvavvake zuciya in tafi da sawu”. Sannan kuma da inda ya ce “Ina da ciki ana ce masa kurumbo” da kuma inda ya ce “hanjina kaca mai kama riga”. Sai inda ya ce “Muna tafiya nakan fizgo kaina, mu faxa kwazazzabo wai shi bai kula ba”.

Duk waxannan zantuttuka na raha ne aka yi amfani da su a zantawar domin a samar da nishaxi da kuma ban dariya.

Har wa yau kuma akwai irin wannan zantawar da ta kasance a tsakanin malam Sanda da keke ta hanyar faxi-in-faxa. Ga yadda ya faxi zantawar a waqar:

Haba! Malami babba kamar ka?
Ba zan iya yada babban malami ba.

Izan dai za ka hau ni, ka tara riga,
Da wando, ba ka hau ni hawan isa ba.

Ya tashi hawa ashe bai tattara ba,
Ya fizgo malamin ba a jinjina ba,

Ya yasai nan da nan a tsakar gidansa,
Cikin matansa tun ba a kai daxe ba.

Ya ce "Bari nai kuren yashe ka, malam,
Za ma ban kai ka bakin kasuwa ba.

Ban na san in ya da mutum na kirki,
Izan ba inda za a yi dariya ba.

Da motsa qararrawarka da kama burki,
Ba za su hana ni in jefad da kai ba.

Ya ce "To, ba ni qara hawanka keke"
Ya ce masa "Ko a dankiya ban kula ba".

Hawan da rashin hawan a gane ni xai na,
Ban ga abin da zai cutad da ni ba.

Kamar tafiya na sauri ko na fizge,
Ba ka je inda ka so nan da nan ba.

Izan ko za ka hau ni ka ba ni iska,
Ka sha, ba inda ba zan je da kai ba.

Ashe ba mai hawa keke ya more,
Izan ba wanda ya iya zanzaro ba.
(Yakawada, 1987:326-327).

Wannan zantawar da Aliyu Namangi ya ambata cewa ta faru a tsakanin malam Sanda da keke duk raha ce kawai. Saboda kowa ya san cewa keke ba ya magana domin shi ba mutum ba ne, kuma ba ya motsi. Amma Aliyu Namangi ya mutuntar da keken yana magana har ma yana amfani da harshen Ingilishi, wato inda yake cewa "Ko a donkiya" (wato bai damu ba). Kowa ya ji wannan ya san raha ce kawai domin a samu nishaxi a kuma yi dariya.

Har wa yau kuma Aliyu Namangi ya bayyana wannan faxi-in-faxa da nufin yi wa malam Sanda ba'a a matsayinsa na abokin wasansa. Kamar inda yake cewa keken ya gindaya masa wasu sharuxa wato idan zai hau keken ya tattara riga da wando, sannan kuma kada ya yi masa hawa na isa.

Saboda haka wannan duk raha ce kawai domin babu yadda za a ce wai keke ne ke gindaya wa mahayinsa sharuxa kafin ya hau shi. Duk wanda ya yi wannan ya san ba'a ce kawai saboda bayan keken ya kayar da malam Sanda sai ya rinqa cewa ya yi kuskure da bai kayar da malam Sanda a bakin kasuwa ba wato inda za a yi masa dariya.

Sannan kuma ko da ya kaxa qararrawa ya kama burki babu abin da zai hana bai kayar da shi ba. Wannan ya qara tabbatar da cewa duk raha ce kawai ta hanyar ba'a mai sigar faxi-in-faxa tsakanin keke da malam Sanda.

Saboda haka a nan za a iya cewa Aliyu Namangi ya yi amfani da nau'o'in raha barkwai guda biyu wato raha barkwai zumuntau da raha barkwai faxi-in-faxa domin yi wa abokan wasansa ba'a saboda ya samar da nishaxi a kuma yi dariya.

4.3 Raha Shaguvau A Wasu Waqoqin Aliyu Namangi

Raha shaguvau wata aba ce, da ake aiwatar da ita domin yin suka ga wasu munanan ayyuka, ko kushe wasu dokokin siyasa, ko falsafar wata al'umma. Aliyu Namangi ya sarrafa raha shaguvau a wasu waqoqinsa domin yin suka ga wasu munanan xabi'u, kamar kwaxayi da rowa da qyuya da qazanta da rashin aiwatar da ibada a kan lokaci. Mawaqin ya yi amfani da wasu zantuttuka na raha wajen aiwatar da sukar domin ya samar da nishaxi a kuma yi dariya. Ga yadda yake cewa a waqoqin:

Ku bar son ba qwalama amana,
Mutum ne, mai halin qaranta.

Yana da kamar dattijo shi kau,

Halinsa na yara ne qanana,

Kwaxai da sata suka qulla kirsa,
Da har suka sa mai yin su kunya.

Don haka ma kogin xayan su,
Baya cika illa bi hammin.

Sun tava aure ma da rowa.
Sai suka haifo xansu rowa".
(Yakawada, 1987:310-312)

Wannan duk suka ce ga waxannan xabi'u marasa kyau domin Allah (S.W.T) ya yi hani da a aikata su. Aliyu Namangi ya mutuntar da waxannan xabi'u tamkar 'yan Adam domin ya nishaxantar da jama'a a waqar. Saboda yadda ya nuna cewa kwaxayi ya auri rowa suka haifi xa sata, sa'annan kuma bayar da amana ga kwaxayi wauta ne saboda rashin gaskiyarsa. Haka kuma qwalama da sata sun qulla amana a tsakaninsu saboda sun amince wa juna.

Waxannan duk zantuttuka ne na raha saboda sanin kowa ne kwaxayi da rowa da sata duk xabi'u ne ba mutane ba. Amma sai ga shi an nuna cewa auratayya da haihuwa da qulla amana sun shiga a tsakaninsu bayan kuwa su ba mutane ba ne xabi'u ne kawai.

Saboda haka, waxanan duk zantuttuka ne na raha kawai domin yin dariya. Duk da cewa wa'azi ne domin a guji aikata ire-iren waxannan xabi'u munana.

Aliyu Namangi ya ci gaba da yin kira ga ire-iren waxannan xabi'u marasa kyau kamar qyuya da saivi da bacci da lalaci da sauran su. Ga dai yadda yake cewa a waqar:

Haka nan, auren qyuya da saivi,
Sai suka haifo xa talauci.

Wannan ko auren hawa ma da bacci,

Sai suka haifo 'ya hasara,

Da hasara ta cika, ta yi nono,
Sai qyuya yaj je bixar ta,

Aka ce mashi tsautsai ya riga ka,
Ya zaka ya nema ma yaro.

Hasara tai auren talauci,
Sai suka haifo xansu bashi.

Ya tashi da safe yana kirari,
Sai shi baqin dunhu xan hasara.

Shi ne dunhu xan hasara,
Wanda ba ya barin mai yinsa jali.

Amma ku bar ni uina tsoron talauci,
Yanda nake tsoron gwagwarci.
(Yakawada, 1987:310).

Wannan ma duk suka ce ga waxannan xabi'u marasa kyau, Aliyu Namangi ya gudanar a wannan waqar, kuma cikin raha da sanya nishaxi ga jama'a. Saboda yadda ya mutuntar da waxannan xabi'u ta hanyar bayyana cewa auratayya da haihuwa sun kasance a tsakanin qyuya da saivi waxanda suka haifi 'yarsu hasara. Bayan hasara ta girma ta isa aure sai qyuya ya je nema wa xansa amma tsautsayi ya riga shi don haka hasara sai ta auri talauci inda suka haifi xa bashi wanda ba ya barin mai yin sa jali.

Waxannan duk zantuka ne na raha kawai Aliyu Namangi ya yi amfani da su domin yin shaguve ga mutanen da ke aikata ire-iren waxannan munanan xabi'u.

Saboda kusan duk wanda ya ji cewa wai qyuya da saivi sun yi aure kuma sun haifi 'yarsu talauci, sa'annan kuma nawa da bacci sun yi aure sun haiufi 'yarsu hasara har ta girma ta isa aure qyuya ya nema wa xansa aurenta amma

tsautsayi ya riga shi. Haqiqa ya san cewa wannan duk raha ce domin a samar da nishaxi a kuma yi dariya. Saboda abubuwan da aka ambata duk xabi'u ne ba mutane ba amma asai aka mutuntar da su aka siffanta su da xabi'un mutane domin a yi dariya.

Har wa yau kuma Aliyu Namangi ya yi suka ga irin xabi'ar nan ta shan taba sigari ta hanyar yin shaguve ga mashaya taba sigari. Ga yadda yake cewa a waqar:

Koda yunwa za ta kan ni,
Har na mutu ba na shan sigari,

Gama bakin mai shan sigari,
In ya san naman karya ya tsotsa.
(Yakawada, 1987:312)

Haqiqa wannan suka ce ga xabi'ar shan taba sigari ta hanyar shaguve cikin raha saboda yadda ya danganta mashayin taba sigari da cin naman kare.

A taqaice dai waxannan su ne baitukan da Aliyu Namangi ya sarrafa raha shaguvau a wannan waqa domin suka ga wasu xabi'u munana tare da gargaxi domin jawo hankulan jama'a da su qaurace musu domin gudun haxuwa da azabar Allah (S.W.T).

Sannan kuma ya yi amfani da wasu zantuttuka na raha a matsayin wani salo na samun damar isar da saqonsa cikin sauqi da nishaxantar da jama'a.

Haka kuma Aliyu namangi ya aiwatar da irin wannan suka a waqarsa ta *Zambon Qazama*. Ga yadda yake cewa a waqar:

Mummunan halin qazama na fari,
Ba ta fyace majina sai da dama.

Hanci majina idanunta kwantsa,
Dattsa ya daxa ma bakinta girma.

Sai ka ga tai jagal da suma da dauxa,
Ga bawali a kwance, tashinta fama.

Bai mai son kitso ba, ta kasa aski,
Taba ya dafe haqoral qazama.
*(*Yakawada, 1987: 323).

Tabbas wannan suka ce ga xabi'ar qazanta ta hanyar shaguve cikin raha ga mata qazamai da su hankalta su daina qazanta a gidajensu da kawunansu.

Aliyu Namangi ya yi amfani da wasu zantuttuka na raha domin ya nishaxantar wajen isar da wannan saqo ga mata qazamai. Saboda yadda ya siffanta qazamar mace da cewa takan fyace majina da hannun dama ga fitsarin kwance. Hancinta duk majina ga idanunta cike da kwantsa, kai ba aski balle kitso da sauransu.

Wannan abin dariya ne da taqaici a sami mace magidanciya mai hankali a cikin wannan yanayi na qazanta.

Saboda haka, wannan shaguve ne cikin raha domin kusan duk wanda ya ji yadda Aliyu Namangi ya siffanta mace qazama a wannan waqa, babu abin da zai hana masa dariya da nishaxi.

Aliyu Namangi ya ci gaba da irin wannan suka ga xabi'ar qazanta ta hanyar shaguve ga mata qazamai. Ga yadda yake cewa a waqar:

Aliyu Namangi ya ci gaba da irin wannan suka ga xabi'ar qazanta ta hanyar shaguve ga mata qazamai a wannan waqa:

Ga yadda yake cewa:

Kwana goma jere, haifar ta goma,
Ba taran miji ga haifar qazama.

Ko bantenta ka qetare sai ta haihu,
In ka san kuxi, su qare a suna.

Ya Allah daxa ma matanmu tsafta,
Ka da Allah ka ba mu mata qazama.
*(*Yakawada, 1987: 324)

Wannan duk suka ce, ga xabi'ar qazanta ta hanyar shaguve cikin raha, saboda komai qazantar mace babu yadda za a ce kullum sai ta haihu har kwana goma a jere, kuma ma ba tare da mijinta ya sadu da ita ba saboda qazanta. Amma da zarar ta tsallake bantensa ta samu ciki ta haihu.

Duk wannan zance ne na raha kawai domin a nishaxantar da jama'a wajen isar da wannan saqo ga mata qazamai.

4.3.1 Raha Shaguvau Mai sigar Wa'azi A Wasu Waqoqin Aliyu Namangi

Raha shaguvau mai sigar wa'azi wani nau'i ne na raha da Aliyu Namangi ya sarrafa a wasu waqoqinsa, domin faxakar da jama'a tare da yin kira da a guji aikata ire-iren waxannan munanan xabi'u da Allah (S.W.T) ya yi hani da a aikata su. Mawaqin ya gargaxi mutane da su guji aikata munanan ayyuka kamar rashin yin sallah a lokacinta da aikata fasadi da matan banza da sace-sace ko rashin yin azumi a watan Ramadan.

Aliyu namangi ya aiwatar da irin wannan suka tare da yin wa'azi a waqarsa ta *Kuntugin Shaixan*. Aliyu Namangi ya samo tushen muryar waqar ce daga ayar Alqur'ani mai girma mai cewa; "La ta lumuni, fa lumu anfusakum" (Suratul Ibrahim: 22).

Wato a lokacin da 'yan wuta za su rinqa cewa shaixan ne ya rinjaye su zuwa ga aikata ayyuka marasa kyau. A inda shi kuma shaixan zai qayata zancensu yana cewa "babu ruwansa kada su zarge shi su zargi kawunansu". Domin an umurce su da su aikata kyawawan ayyuka amma suka bijire wa faxin Allah

(S.W.T). daga nan sai shexan ya kaxa molonsa yana shewa yana yi wa ‘yan wuta gwalo yana cewa:

Aha yayyayye, aha ye iya,
Ursatu ku bar zargi na.

Da an maku doka kun qi ji,
Kukai aiki mummuna.

Aka sa ku ibada kun qiya,
Halinku ya zam tamkana.

Ana sallah da subahi,
Ku sai ku yi taku da rana

Azahar, la’asar, ba ku yi su ba
Sai tare da faxin rana

Magrib, issha ba ku san su ba,
Sai ku harqi tuwo kui kwana.

Da yin asalatu ku qanqame,
Mata da jima’i, kwana.

Wankan janaba ba ku santa ba,
Sai kun yi zufa daga gona.

Watan Ramalan in ya tsaya,
Sai ku shari huranku da rana

Komai na sahur a ci duk da ku.
Ku ji qarfin aikin gona.

Zakka ku qi ba almajirai,
Sai ku ba makaxa kui suna.

Kuxinku ku kai ma karuwai,
Ku dinga fasadi kwana.

(Yakawada, 1987: 308-309)

Wannan duk shaguve ne ta sigar wa’azi ga jama’a da su hankalta su guje wa aikata munanan ayyuka waxanda Allah (SWT) ya yi hani da a aikata su.

Aliyu Namangi ya kawo ire-iren waxannan munanan ayyuka domin a qaurace masu gudu saboda haxuwa da azabar Allah (S.W.T). waxannan laifuka kuwa sun haxa da rashin yin sallah a lokacinta da rashin azumin watan Ramadan da kuma mutanen da ba sa tsarkake jikinsu bayan sun sadu da iyalansu (wato wankan janaba).

Aliyu Namangi ya ci gaba da bayyana yadda wasu ba sa iya bayar da zakka ga mabuqata, sai dai su tafi da kuxinsu ga karuwai suna fasadi. Wannan duk shaguve ne da sigar wa'azi ga jama'a Aliyu Namangi ke yi ta hanyar amfani da wasu zantuttuka na raha domin ya nishaxantar wajen isar da saqon da ke qunshe a waqarsa. Saboda abin dariya ne a samu babban mutum magidanci yana sallar asubahi bayan fitowar rana ko sallar azahar da la'asar bayan faxuwar rana, ko kuma a samu mutum magidanci bai san sallar magariba da issha ba, sai dai kawai ya harqi tuwo ya kwanta. Da kuma mutanen da suke qanqame iyalansu da jima'i kuma ba sa yin wankan janaba sai dai sun dawo daga aikin gona suke yin wanka, amma ba domin janabar da ta ke tare da su ba.

Saboda haka, wannan duk abin dariya ne a samu mutum magidanci da ire-iren waxannan xabi'u musamman ma a qasar Hausa.

Wani abin dariya da sanya nishaxi a waqar kuma shi ne yadda Aliyu Namangi ya bayyana yadda wasu magidanta ke goranta wa iyalansu game da kuxin cefane da daddawa da gishiri, kawai domin sun tambaye su kuxin kitso. Ga yadda yake cewa a waqar:

Matanku su roqi kuxin kitso,
Ka ji "Ba ni wuri tsinanna!

Ai na san ba ki da hankali,

Dominki in bar sha'anina?

Gishiri, dadawa da kuxin awo,
Duka sai in fitar a jakana.

Kana in ba ki kuxin kitso,
Ga cinki da sha a jikina".
*(*Yakawada, 1987: 308-309)

Haqiqa wannan abin dariya ne da nishaxi a samu mutum magidanci na goranta wa iyalansa kan kuxin cefane da daddawa da gishiri, domin sun tambaye shi kuxin kitso.

Wannan shaguve ne da sigar wa'azi kuma cikin raha Aliyu Namangi ke yi domin ya nishaxantar wajen isar da saqon da ke qunshe a waqarsa.

Haka kuma Aliyu namangi ya yi irin wannan suka ta hanyar wa'azi a waqarsa ta *Tambihul Anami* (Faxakar da jama'a), mawaqin ya wallafa wannan waqa ce da nufin wa'azi ganin yadda wasu mutane ke savawa Allah (S.W.T). wannan yasa Aliyu Namangi ya fara gabatar da wannan waqa ba tare da ya buxe waqar da basmala ba. Ga yadda yake cewa a waqar:

Har haka nai istingifari,
Da aure in mace ke walicci.

Amre ba yardan waliyyi,
Shi ke sa haifar xa shaqiyyi.

Wata rana na cewa malaminmu,
Muhammadu ban san wawuta ba.

Ya yi batun wauta a nafsi,
Za mu faxi kowa ya qirga.

Da wanda yakan ga gida ya faxa,
Shi bai sallama an ce "shigo" ba.

Amma ko ba na salati,
Hali uku ban gane da su ba.

Ba ni ganin dabba a turba,
Zai mutu in taka, in yanka.

Kowa ke wannan xabi'a,
Zuwa gaba sa zauna a yari.

In ka ji ana "ku tare varawo",
Da za ka tare ka iske shi ne.

Ba ni ganin mace ta yi yaji,
In je in tare ta ina ta biko.

Mai bikon matan mutane,
Zuwa gaba sa tara da gora.

Ko da yunwa za ta kan ni,
Har na mutu ba na shan sigari.

Gama bakin mai shan sigari,
In ya san naman karya ya tsotsa.

*(*Yakawada, 1987: 310-312)

Waxannan duk wasu xabi'u ne marasa kyau Aliyu Namangi ke faxakar da mutane illolinsu ta hanyar shaguve cikin raha domin ya nishaxantar da jama'a.

Aliyu Namangi ya bayyana wasu munanan xabi'u uku cikin raha, domin yin shaguve ga masu aikata ire-iren waxannan xabi'u kamar masu kama dabbobin mutane su yanka da masu neman matan aure, da kuma mashaya taba sigari.

Waxannan duk xabi'u ne marasa kyau da Aliyu Namangi ya kawo cikin raha domin ya nishaxantar, kasancewar yadda ya gabatar da su a cikin waqar. Wato kamar inda ya nuna duk mai xabi'ar yanka dabbobin mutane zuwa gaba zai zauna da yari, kuma in ka ji ana "ku tare varawo", da za ka tare ka iske shi ne.

Haka kuma duk mai bikon matan mutane zuwa gaba sa tara da gora. Sannan kuma ko da yunwa za ta kar shi, har ya mutu ba ya shan taba sigari. Saboda duk mai shan taba sigari in ya samu naman karya zai tsotsa.

Waxannan duk zantuttuka ne na raha, Aliyu Namangi ya yi amfani da su wajen shaguve domin ya yi suka ga ire-iren waxannan xabi'u munana.

Saboda haka, wannan shaguve ne da sigar wa'azi cikin raha da nishaxi, Aliyu Namangi ke yi domin isar da saqon da ke qunshe a waqarsa.

4.4 Kammalawa

Wannan babi ya kammala bayan an yi bayani dangane da yadda Aliyu Namangi ya sarrafa wasu na'o'in raha a wasu waqoqinsa. Bayan haka kuma an yi xan taqaitaccen bayanin asalin samuwar waqoqin tare da yin tsokacin wuraren da mawaqin ya yi amfani da zantuttuka na raha domin ya nishaxantar da jama'a.

Har wa yau kuma babin ya sama da wasu bayanai game da nau'o'in rahar da Aliyu namangi ya sarrafa a waqoqin wato kamar raha barkwai da raha shaguvau da kuma raha faxi-in-faxa. Sai kuma sharhi dangane da wuraren da aka samu rahar a waqoqin.

BABI NA BIYAR

NAXEWA

5.0 Gabatarwa

A wannan babi wanda shi ne babi na qarshe a wannan aiki wanda za a naxe shimfixar wannan bincike. Sannan kuma za a bayyana yadda aka aiwatar da wannan aiki daki-daki.

Haka kuma a wannan babi ne za a bayyana sakamakon abubuwan da wannan bincike ya gano domin kawar da hasashen da ake yi game da manufar Aliyu Namangi ta yin amfani da wasu zantuttuka na raha a wasu waqoqinsa. Har wa yau kuma duk a wannan babi ne za a bayar da wasu ‘yan shawarwari musamman ma ga ‘yan uwa xalibai da sauran manazarta da kuma marubuta waqoqin Hausa.

5.1 Kammalawa

Nazarin rubutattun waqoqin Hausa na da matuqar muhimmanci, musamman ma a wannan fage na ilimi, idan aka yi la’akari da ire-iren saqonnin da ke qunshe a waqoqin. Saboda mawaqan kan aiwatar da waqoqinsu ne domin faxakarwa ko wa’azantar da jama’a.

A wannan bincike mai suna *Raha A Wasu waqoqin Aliyu Namangi* a inda aka nazarci waqoqin da mawaqin ya sarrafa raha a cikin su. An gano cewa Aliyu

Namangi ya sarrafa raha nau'i uku ne a waxannan waqoqi da aka nazarta. Wato raha barkwai da raha shaguvau da kuma raha faxi-in-faxa.

Haka kuma binciken ya gano cewa Aliyu Namangi ya sarrafa raha barkwai ne, domin ya qara qarfafa zumuncin da ke tsakaninsa da 'yan'uwansa ta hanyar yi musu ba'a a waqoqin, kasancewar akwai wasan barkwanci na zumunta a tsakaninsu. Sa'annan kuma ya sarrafa raha shaguvau domin ya yi suka ga wasu xabi'u munana.

Binciken ya gani cewa raha na da matuqar muhimmanci ga rayuwar al'ummar Hausawa ta yin la'akari da yadda Aliyu Namangi ya sarrafa rahar a wasu waqoqinsa, domin ya nishaxantar da jama'a.

Wannan bincike ya tabbatar da cewa mawaqa kan yi amfani da kowani irin salo da ka iya sanya waqarsu ta karvu cikin sauqi. Domin Aliyu Namangi, ya yi amfani da wasu zantuttuka na raha domin ya samar da nishaxi a kuma yi dariya.

Har wa yau kuma wannan bincike ya gano cewa zantuttuka na raha wata hikima ce ta isar da wasu saqonni cikin nishaxi ba tare da wata gundura ba, savanin yadda wasu ke kallon zantuttuka na raha a matsayin wasa ko shiririta.

Binciken ya yi amfani da ra'in isar da saqo ya gano cewa manufar Aliyu namangi ita ce ya isar da saqon da ke qunshe a waxannan waqoqi da aka nazarta, ke nan wannan wani salo ne na jawo hankali ta hanyar raha da nishaxi.

5.2 Shawarwari

A wannan muhalli, wannan bincike zai bayar da wasu ‘yan shawarwari ne waxanda za su taimaka wajen faxaxa bincike da kuma inganta shi a fage na adabin rubutacciyar waqar Hausa.

Shawara ta farko dai ita ce ga ‘yan uwa xalibai manazarta harshen Hausa, kuma musamman ma ga masu sha’awar gudanar da bincike game da rubutattun waqoqin Hausa. Da su xora bincikensu ga ire-iren waxannan waqoqi masu qunshe da zantuttuka na raha, domin an fahimci cewa suna da matuqar muhimmanci wajen nishaxantar da jama’a, sa’annan kuma akwai qarancin bincike ga ire-iren waxannan waqoqi na Hausa.

Haka kuma yana da kyau a qara yawaita bincike game da ire-iren waxannan waqoqi masu qunshe da zantuttuka na raha domin kusan duk ayyukan da aka ci karo da su kan raha, sun fi karkata ne ga wasannin kwaikwayo na Hausa da kuma qagaggun labarai na Hausa. Wannan ya tabbatar da cewa an fi mayar da hankali ga waxannan vangarori a duk lokacin da za a gudanar da wani bincike game da raha ko nishaxi.

Dangane da kafafen yaxa labarai kuwa, musamman ma gidajen rediyo da na talabijin, ana bayar da shawara da su qoqarta wajen yawaita sanya ire-iren waxannan waqoqi masu qunshe da zantuttuka na raha saboda yin hakan zai taimaka matuqa wajen nishaxantar da jama’a, sa’annan kuma ‘yan baya su amfana da wasu zantuttuka na raha da ba su san da su ba.

Har wa yau kuma ga wata shawara ga cibiyoyin binciken al’adu da hukumomin adana kayayyakin tarihi da al’adun gargajiya da kuma jami’o’i da sauran manyan makarantu da sarakunan al’ummu da manyan masana kuma

marubuta, da su tallafi wannan fanni wajen taskace ire-iren abubuwan da aka gano game da raha domin a kange su daga salwanta.

A qarshe wannan bincike na bayar da shawara ga marubuta waqoqin Hausa da kuma mawaqan baka na Hausa da su qoqarta wajen yin amfani da irin wannan salo na zantuttuka a lokacin gudanar da waqoqinsu. Hakan zai taimaka wa jama'a wajen yawaita sauraran waqoqinsu, sa'annan hakan zai sanya a samu sauqin fahimtar saqon da ke qunshe a waqar ba tare da sun gundura da sauraron ko karanta waqoqin ba.

5.3 Naxewa

Wannan bincike ya qunshi babi-babi har guda biyar, wato dai a inda aka kawo abubuwan da wannan bincike ya qunsa kamar yadda ya gabata. A babi na xaya akwai abubuwan da suka haxa da dalilan bincike da muhimmancin bincike da farfajiyar bincike da hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan bincike. Haka kuma babin ya qunshi taqaitaccen tarihin Aliyu Namangi wanda binciken ya gudana a waqoqinsa.

Babi na biyu kuwa waiwaye aka yi game da ayyukan da suka gabata, domin yin tsokaci tare da samun haske daga gare su, saboda sanin inda alqiblar wannan aiki ta dosa.

A babi na uku kuwa an bayyana yadda Aliyu Namangi ya sarrafa raha barkwai a wasu waqoqinsa, domin nuna muhimmancin zumunta a tsakanin al'umma. Shi kuwa babi na huxu ya gudana ne ta hanyar bayyana yadda Aliyu Namangi ya sarrafa raha shaguvau a wasu waqoqinsa.

Sai babi na biyar inda aka naxe tabarmar wannan bincike, aka kuma taqaita bayanan abubuwan da binciken ya qunsa tare da bayar da wasu ‘yan shawarwari waxanda ake ganin cewa za su taimaka wajen ci gaba da gudanar da bincike game da abubuwan da suka shafi raha a rayuwar Bahaushe.

Manazarta

Abubakar, M. (2007) “Raha A Rubutaccen Wasan Kwaikwayon Hausa: Sharhi A Kan Littafin, *Malam Inkuntum*. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Abdullahi, S. (1995) “Yabo Da Habaici A Rubutattun Waqoqi”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Abrams, M.H. et al, (2009) *A Glossary of Literary Terms* (9th edition) U.S.A: Wardsworth Cengage Learning Boston.

Adebayo, C.O. (1995) "The Language of Comedy In Nigerian Television Authority Ilorin Art Its Importance To Its Immediate Environment A Semantic Approach. Zariya: Ahmadu Bello University

Aminu, M.L. (1992) "Poetry And Political Ideology: A Glimpse Of Arewa Jumhuriya ko Mulukiya Of Sa'adu Zungur" Muqala Da Aka Gabatar A Taron Qara wa Juna Sani. Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka: Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Aminu, H. (2012) "Raha A Wasan Kwaikwayon Hausa: Kwatancin Wasannin Karambana Da Wasu Na Xan Ibro" Kundun Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Auta, A.L. (2008) "Rubutattun Waqoqin Hausa Na Faxakarwa A Qarni Na Ashirin, Kundin Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Vavura, S. (1983) *Barkwanci* Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya Kano: Jami'ar Bayero.

Bayero, A.Y. (2004) "Rubutattun Waqoqin Nasiha: A Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa Na Wa'azi?" A cikin *Algaita.* Journal of Current Research In Hausa Studies Vol. 3, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya: Kano: Jami'ar Bayero.

Birniwa, H.A. (1981) *The Imfiraji I & IV Of Aliyu Namangi* Kundin Digiri Na Biyu, London: Jami'ar SOAS.

Birnin-Tudu, S.Y. (2002) "Jigo Da Salon Rubutattun Waqoqin Furu'a Na Qarni Na Ashirin" Kundin Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami'ar Usman Xanfodiyo.

Bargery, G.P. (1993) *A Hausa English Dictionary And English Hausa Vocabulary.* Zaria: Ahmadu Bello University Press, Limited.

Brown, A.R. (1952) *Structure and Function in Primitive Society* Essay and Address. London: W.J. Cotton & West LNopercy Street.

C.N.H.N (1977) *Waqa A Bakin Mai Ita* (Littafi Na Xaya), Zariya, N.N.P.C.

C.N.H.N (1979) *Waqa A Bakin Mai Ita* (Littafi Na Biyu) Zariya, N.N.P.C.

C.N.H.N (2006) *Qamusun Hausa* Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano, Jami'ar Bayero.

Crow, B. (1983) *Studying Drama:* Nijerian Longman.

Xangambo, A. (1973) “Aliyu Namangi Da Waqoqinsa”, Kundin Digiri Na farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano Jami’ar Bayero.

Xangambo, A. (1974) *The Poetry Life And Opinion of Sa’adu Zungur*. Zariya: Northern Nijera Publishing Company.

Xangambo, A. (1979) *Zavavvun Waqoqin Da Da Na Yanzu.* Lagos: Thomas Nelson Nigeria Limited.

Xangambo, A. (1980) “Hausa Wa’azi Verse, From C.A. 1800 To C.A. 1970, Study of Form, Content, Language and Style. Kundin Digiri Na Uku, School of Oriental And African Studies London

Xangambo, A. (1981) “Rikixar Azanci: Siddabarun Salo Da Harshe A Cikin Waqar Tabarqoqo, Tahamisin Aliyu Xansidi. A Cikin Studies in Hausa Language Literature And Culture, Kano: Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Xangambo, A. (2007) *Xaurayar Gadon Fexe Waqa.* Zariya: Amana Publishers

Xangambo, A. (2008) *Rabe-Raben Adabin Hausa* (Sabon Tsari). Zariya: Amana Publishers

Dunfawa, A.A. (1990) “Gudummuwar Masu Xariqa Wajen Havaka Rubutattun Waqoqin Hausa” Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka, Zariya, Jami’ar Ahmadu Bello.

Dunfawa, A.A. (2004) “Zuga A Cikin Waqoqin Fada” *Algaita* Journal of Current Research In Hausa Studies No: 3 Vol. 1. Kano: Jami’ar Bayero.

Dunfawa, A.A. (2004) “Waqa A Tunanin Yara”, Kundin Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Sakkwato: Jami’ar Usman Xanfodiyo.

Diji, R.J. (2004) *Understanding Poetry 2: An Anthology of Poems for Schools and Colleges*, Zariya: Enifab Graphic Press.

Xan’iya, D. (1997) “Adon Harshe Cikin Rubutaccen Adabin Hausa”. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Xahiru, M. (1986) “Rayuwa Da Zantuttukan Hikimar Muhammadu Na Almamowa Funtua”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami’ar Usman Xanfodiyo.

Xiso, A.H. (1997) "Zambo Da Yabo A Matsayin Dabarun Jawo Hankali A Rubutattun Waqoqin Siyasa": Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Eagle, D. (1970) *Concise Oxford Dictionary of English Literature*: London: Oxford University, Press.

Furniss, G. (1996) *Poetry, Prose And Popular Culture in Hausa*. London: Edinburg, University Press

Frye, M. (1957) Anatomy of Criticism: Princeton, University, Press.

Gaya, A.S. (1972) "Comparison Between Mu'azu Haxeja And Sa'adu Zungur" Kundin Digiri Na farko, Sashen Nazarin Harsunn Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (1988) "Waqoqin Makaxan Fada: Sigoginsu Da Yanayinsu Musamman a Qasar Sakkwato", Kundin Digiri Na Uku, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2002) "*Wasu Sanabe-Sanaben Rubutu Da Nazarin Rubutattun Waqoqin Hausa*" A Cikin *Algaita,* Journal of Current Research In Hausa Studies series III Vol. 2 No. 6 2002 Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Gusau, S.M. (2011) "Ga Fili Ga Mai Doki: Wata Mahanga Ga Mawaqa Da Makaxan Hausa". Takarda Da Aka Gabatar A taron Qara wa Juna Sani Na Haxin Gwiwa Tsakanin Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Ta kano Da Hukumar Tace Finafinai Da Xab'i Ta Jihar Kano.

Hassan, U. (1973) "Alhaji Aliyu Namangi: A Survey of His Biography Sources And Features of His Major Works" Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Hiskett, M. (1975) *A History of Hausa Islamic Verse,* London: SOAS.

Hiskett, M. (1981) "Towards A Comparison of Theme And Style in Hausa Verse Categories of Wa'azi And Madahu" A Cikin Studies in Hausa Language, Literature And Culture (5th Hausa International Conference) Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Isma'il, A. (1994) "Rubutattun Waqoqi A Qasar Kano: Nazarin Waqoqin Yabon Annabi (S.A.W)". Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Kano. Jami'ar Bayero.

Isa, A.S. (2007) "Raha A Wasan Qasimu Yero: Tarken wasanin Karambana". Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Iliyasu, M. (1995) "Gaskiya Da Raha A Cikin Littafin *Ruwan Bagaja*. Sharhi Ciki Da Waje". Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Katsina, Y.A. (1984) "Labaran Raha Da Muhimmancinsu Ga Hausawa", Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

McGrow-Hill (1972) *Encyclopedia of World Drama* Vol. 4 London: McGrow-Hill.

Meredith, G. (1977) *An Essay on Comedy*. New York: Charls Scribers Sons

Muhammad, D. (1973) "Sharhin Hausa Mai ban Haushi Ta Aqilu Aliyu" A Cikin Harsunan Nijeriya Vol. 3. Kano: Centre For The Study of Nigeria Languages.

Muhammad, D. (1985) "Visual Imagery in Blind Poetry Illustrations From Namangi's *Imfiraji* And Audu Makaho's Tabuka" Maqala A cikin Magazine. Lagos, Nigeria.

Muhammad, S.S. (2010) *Bazazzagiya*. Zariya. Maigodo Multi Media.

Muhammad, S.S. (2011) "Kwatancin Waqar *Jiddul Ajizi* (Qwazon Gajiyayye)" Ta Malam Shitu Xan Abdurra'ufu Da Waqar Kanzil Azim (Babbar Taska) Ta Malam Aliyu Namangi Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Nazarin Harsuna Da Al'adun Afirka. Zariya: Jami'ar Ahmadu Bello.

Mukhtar, I. (2005) *Bayanin Rubutattun Waqoqin Hausa.* Abuja: Country Sides Publishers Company.

Muktar, I. (2006) "Gudummuwar Rubutattun waqoqin Hausa Wajen Adana tarihin Siyasar Nijeriya" *Algaita* No. 4 Vol. 1 Kano: Benchmark Publishers Limited.

Malumfashi, A.I. (1984) “Wa’azi A Rubutattun Waqoqin Qarni Na Ashirin” Takarda da Aka Gabatar A taron Qara wa Juna Ilimi. Sakkwato: Hukumar Fasaha Da Al’adun gargajiya.

Musa, U.J. (2008) “Raha A wasan Kwaikwayon Shiga Sharo Ba Shanu” Na N.T.A Kaduna”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Nazifi, M.M. (2011) “Atharul-Lugatul Arabiyyati Fi Shi’iri Hausa: Aliyu Namangi”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Namangi, A.A. (1972) *Waqoqin Imfiraji Juzu’i 1-9*, Zariya: N.N.P.C.

Namangi, A.A. (1992) “Waqar Furan Gero Da *Tsarabar Madina*. Zariya: N.N.P.C.

Nafi’u, H.M. (2000) “Auratayyar Salo: Nazari Kan Tarbi’i Da Tahamisi A Rubutattun Waqoqin Hausa”. Kundin Digiri Na Biyu. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Othman, J.A. (1975) “Waqoqin Qarni Na Ashirin Da Jigoginsu” Kundin Digiri Na Farko. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Satatima, I.G. (1999) “Tarsashin Adabin Baka Cikin Rubutattun waqoqin Hausa” Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Sa’id, B. (2002) “Rubutattun Waqoqin Hausa Na qarni Na Ashirin A Jihohin Sakkwato Da Kebbi Da Zamfara. Kundin Digiri Na Uku. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Sa’id, B. (1995) “Tasirin Larabci A Kan Rubutattun Waqoqin Hausa”, Maqala da Aka Gabatar A kan Harshe Da Adabi Da Al’adun Hausa. Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Sa’id, B. (1981) “Gudummuwar masu Jihadi A Kan Adabin Hausa” Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Sankalawa, D.H. (2005) “Kwatanta Wasu waqoqin Aliyu Namangi Da Takwarorinsu Na Sani Yusuf Ayagi”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Sani, A. (1993) “Wasan Raha A Tsakanin Masu Sana’o’i A qasar Hausa”. Kundin Digiri Na Farko, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Stephen, M. (2006) *English Literature A Student Guide:* London: Pearson Education Limited.

Sambo, M.B. “Gudummuwar Shehu Jibrin Golovo Ga Bunqasar Wasan Kwaikwayon Raha A Hausa”. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami’ar Usman Xanfodiyo.

Skinner, N. (1969) “A Hausa Poet In Lighter Vein”. Muqala A African languages Review.

Skinner, N. (1971) “The Slattern A Theme of Hausa Poetry” Africanische Sprache And Kuturen Band 14,

Skinner, N. (2004) *Qamus* Na Turanci Da Hausa. Zariya: The Northern Nigerian Publishing Limited.

Talle, B.A. (1990) “Baki Abin Magana: Nazari A Kan Hikimomin Muhammadu Na Almamowa Funtuwa”. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka, Zariya, Jami’ar Ahmadu Bello

Wilson, E & Godfarb, A. (2002) *Theatre The Lively Art*. London: McGrow-Hill.

Yahaya, A.B. (1995) “Siffantarwa Bazar Mawaqa, Wani Saqo A Kan Nazarin waqa” . Takarda Da Aka Gabatar A Taron Qara wa Juna Ilimi A Kan Harshe Da Adabi Da Al’adun Hausa. Kano: Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’ar Bayero.

Yahaya, A.B. (2004) “Rubutattun waqoqin Nasiha, Wani Vangare Ko Kuwa Sauyin Salo A Cikin Rubutattun Waqoqin Hausa Na Waziri” *Algaita* Journal Of Current Research In Hausa Studies No.3 Vol. 1. 2004

Yahaya, A.B. (2001) *Salo Asirin Waqa*, Kaduna Fisba Media Service.

Yahaya, I.Y. (1988) *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubuce Cikin Hausa*. Zariya: N.N.P.C.

Yakawada, M.T. (1987) “Tarkakken Matanin Waqar *Kanzil Azimi*” Ta Aliyu Namangi. Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka: Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello.

Yakasai, B.L. (1984) “Rayuwar Alhaji Na’ibi Suleiman Wali Da Waqoqinsa” Kundin Digiri Na Farko, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Kano: Jami’ar Bayero.

Yahaya, A.B. (1997) *Jigon Nazarin waqa,* Kaduna Fisbas Media Services

Yahaya, A.B. (1988) “Qawancen Jigo Tsakanin Waqoqin Baka Da Rubutattu”, Takardar da Aka gabatar A Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya. Sakkwato: Jami’ar Usmanu Xanfodiyo.

Zubairu, U. (1992) “Wasan Raha A Hausa”, Kundin Digiri Na Biyu, Sashen Harsuna Da Al’adun Afirka. Zariya: Jami’ar Ahmadu Bello

Ratayen waqoqin da aka nazarta

Waqar *Basukur*

1. Muna shukura ga Rabbal alamina,
   Da alhairin da yai mana ba kaxan ba.

2. Muna murna da mulkin Ingilishi,
   Zuwad da sukai qasarmu ba tai tsiya ba.

3. Zama zamaninsu ne aka zo da faifa,
   Kuxi ba masu nauyaya aljihu ba.

4. Daxa zarafinsu ne aka zo da jirgi,
   Ka je Maka ba da tashin hankali ba.

5. Sa'an nan ga su babur ga su mota,
   Da farko da a can ba mu san da su ba.

6. Izan tafiya ta faru, ka nemi mota,
   Izam jirgi ba kui daidai da shi ba,

7. Izan kawa babu jirgi babu mota,
   Ka je da qafarka, ba keke tsiya ba.

8. Ban ni da *Basukur*, ho xan jidali,
   Shaqiyi, ba abin babba ya hau ba.

9. A Xanmahawayi nih hau, sai ya bar ni,
   Tudun Yakaji ban kawo gari ba.

10. Ya bar ni da jin jiki da zama a turba,
    Dabai ko Jumma'a ba a je da ni ba.

11. Kuxi tirmis na ba shi sule da sisi,
    Keke bai mini rangwame ko da xari ba.

12. Na ce masa "*Basukur*, riqa sawwaqewa"
    Yace "Malam hala ba ka san ni ne ba.

13. Ina da tsiya biyar: farkonsu fanca,
Nakan buga bindiga ba mai wuta ba.

14. Im vavvake zuciya in tafi da sawu,
Cikin daji kamar ba a je da ni ba.

15. Muna tafiya, nakan kuma fizge kaina,
Mu faxa kwazazzabo, ni ban kula ba.

16. Ina da ciki ana ce mai kurumbo,
Karambanin hawa ba ka saya ba.

17. Hanjina kaca mai kama riga,
Mu fizgo mai hawa ni ban kula ba.

18. Tsiya na can, mu je bisa kan kadarko,
Maxaixaici, in ce ba za mu hau ba.

19. In hau bisa kafaxar mahayi in zauna,
Kamar mahayin daxai bai hau ni shi ba”

20. Sukai kadda da Sale a kan kadarko,
Sai ya ce “Haba Sale ba zan ya da kai ba”.

21. Garin suka wantsala haka, kan ya qwace
Ashe ba Sale ne a cikin ruwa ba?

22. Ya bi shi ya bangaje, ya buge, yana ce,
“A zo a gani izan ban ya da kai ba”.

23. Malam Sale sai da ya tuve riga,
Ya sa ka ga Sale har bai sha ruwa ba.

24. Ya tashi ya hau tudu, keke ya bi shi.
Da rigar Sale keke bai saka ba.

25. Su malam Sanda duk suka tar ma keke
Da ban magana, ya ce ba zai sako ba.

26. Ya ma rantse da jirgi da mota,
Wai ba za shi sako izan ba a sa wuqa ba.

27. Malam Sanda sun shirya da keke,
Wai yana qaunar sa ba domin tsiya ba.

28. Ya ce “Haba! Malami babba kamarka?
Ba zan iya ya da babban malami ba.

29. Izan dai za ka hau ni, ka tara riga,
Da wando, ba ka hau ni hawan isa ba.

30. Ya tashi hawa ashe bai tattara ba,
Ya fizgo malamin ba a jinjina ba.

31. Ya yasai nan da nan a tsakar gidansa,
Cikin matansa tun ba a kai dave ba.

32. Ya ce “Bari nai kuren yashe ka, malam,
Zama ban kai ka bakin kasuwa ba.

33. Ban na san in ya da mutum na kirki,
Izan ba inda za a yi dariya ba.

34. Da motsa qararrawarka da kama burki,
Ba za su hana ni in jefad da kai ba.

35. ya ce “To, ba ni qara hawanka, keke”
Ya ce masa, “Ko a dankiya ban kula ba.

36. Hawan da rashin hawan a gare ni xai na,
Ban ga abin da zai cutad da ni ba.
37. Kamar tafiya na sauri ko na fizge,
Ba ka je inda ka so nan da nan ba.

38. Izan ko za ka hauni ka ba ni iska,
Ka sha, ba inda ba zan je da kai ba”.

39. Ashe ba mai hawa keke ya more.
Izan ba wanda ya iya zanzaro ba.

Waqar Tambihul Anani (Faxakar Da Jama'a)

1. Ku bar son ba qwalama amana
   Mutum ne mai halin qaranta

2. yana da kamar dattijo shi kau
   halinsa na yara ne qanana

3. kwaxai da zato suka qulla kirsa
   da har suka sa mai yin su kunya

4. don hakana kogin xayansu
   ba ya cika illa bi hammin

5. Sun tava aure ma da rowa
   Sai suka haifo xansu sata

6. Hakanan auren qyuya da saivi
   Sai suka haifo xa talauci

7. Wannan ko auren nawa ma da bacci
   Sai suka haifo 'ya hasara

8. Da hasara ta cika ta yi nono
   Sai qyuya yaj je bixan ta

9. Aka ce mashi tsautsai ya riga ka
   Ya zaka ya nema ma yaro

10. Hasara tai auren talauci
    Sai suka haifo xansu bashi

11. Ya tashi da safe yana kirari
    Sai shi baqi dunhu xan hasara

12. Shi ne dunhu xan hasara
    Wanda ba ya barin mai yin sa jali

13. Amma ku ban ni ina tsoron talauci
    Yanda nake tsoron gwagwarci

14. Abin da suke jawo wadata
Malam ya ce su xari ne

15. Kyaukyawa ya xebi goma
Mai fara'a ya xebi goma

16. Mai kyauta ya xebi goma
Ya bar saba'in sarki ya kwashe

17. Abin da suke jawo talauci
Malam ya ce su xari ne

18. Mummuna ya xebi goma
Marar fara'a ya xebi goma

19. Mai rowa ya xebi goma
Ya bar saba'in gwauro ya kwashe

20. Har haka nai istingifari
Da aure in mace ke wakilci

21. Amre ba yardan waliyi
Shi ke sa haifar xa shaqiyi

22. wata rana na cewa malaminmu
Muhammadu ban san wawuta ba,

23. Ya yi batun wauta a nafsi
Za mu faxi kowa ya qirga

24. Da wanda yakan ga gida ya faxa
Shi bai sallama an ce "shigo" ba

25. Amma ko ba na salati
Hali uku ban gane da su ba

26. Ba ni ganin dabba a turba
Zai mutu in taka in yanka

27. Kowa ke wannan xabi'a
Zuwa gaba sa zauna da yari

28. In ka ji ana ku tare varawo
Da za ka tare ka iske shi ne

29. Ba ni ganin mace ta yi yaji
In je in tare ta ina ta biko

30. Mai bikon matan mutane
Zuwa gaba sa tara da gora

31. Ko da yunwa za ta kan ni
Har na mutu ba na shan sigari

32. Gama bakin mai shan sigari
In ya san naman karya ya tsotsa

Waqar Kuntigin Shaixan

1. Aha yayyayye, aha ye iya,
   Ursatu ku bar zargi na.

2. Da an maku doka kun qi ji
   Kukai aiki mummuna.

3. Aka sa ku ibada kun qiya
   Halinku ya zam tamkana

4. Ana sallah da subahi
   Ku sai ku yi taku da rana

5. Azahar, la'asar, ba ku yi su ba
   Sai tare da faxin rana

6. Magriba, issha ba ku san su ba
   Sai ku harqi tuwo kui kwana

7. Da yin asalatu ku qanqame,
   Mata da jima'i, kwana

8. Wankan janaba ba ku santa ba,
   Sai kun yi zufa daga gona.

9. Watan Ramalan in ya tsaya,
   Sai ku shari hurarku da rana.

10. Komi na sahur a ci duk da ku,
    Ku ji qarfin aikin gona.

11. Zakka ku qi ba almajirai,
    Sai ku ba makaxa kui suna.

12. Kuxinku ku kai ma karuwai,
    Ku dinga fasadi kwana.

13. Matanku su roqi kuxin kitso,
    Ka ji "Ba ni wuri tsinanna!

14. Ai na san ba ki da hankali
Dominki in bar sha'anina?

15. Gishiri, dadawa da kuxin awo,
Duka sai in fitar a jakana.

16. Kana in ba ki kuxin kitso,
Ga cinki da sha a jikina".

17. Da gamo da abokanni ka ce
"Yau na so dukan matana

18. Ka san Gude ba ta da hankali
Ita ke neman tono na

19. Wai sai in ba ta kuxin kitso
Ga buki a gidan surukina"

20. Aka ce ma Shata na zuwa
Gun vad da kuxi kai suna

21. Da ma sha'anin ya matso zuwa,
Ga akawu na kai kekena.

22. Jinginarta na karvo fan tara,
Domin in kar gararina.

23. Da ganin makaxi in ce masa,
Ya yi min taken kakana"

24. Takensa bixa qi-tanqwasa
Falali sha qunan rana.

25. Bunsuru ka aure uwa da 'ya,
Shabara kutunkun vauna.

26. Dabba ba ka san na qoshi ba,
Doki mai tauna kwana.

27. Raman karakande rashin faxa,
Qibanka husuma kwana.

Waqar Zambon *Qazama*

1. Ya Allahu, Rabbana taimake mu,
   Mu gargaxi ‘yan’uwa da auren *Qazama*,

2. Auren tsohuwa hasara ga yaro,
   Gwammaci tsohuwa da auren *Qazama*.

3. In ba ka san ta ne ba kau tambaye ni,
   In Allah ya yarda ka san *Qazama*.

4. Mummunan halin *Qazama* na fari,
   Ba ta fyace majina sai da dama.

5. Hanci majina, idanunta kwantsa,
   Dattsa ya daxa ma bakinta girma.

6. Sai ka ga tai jagal da suma da dauxa,
   Ga bawali a kwance, tashin ta fama.

7. Ba mai son kitso ba, ta kasa aski,
   Taba ya dafe haqoral *Qazama*.

8. Gude ba qoqari ba, ga kasa girki,
   Ga haxama a zuci, qoshinta fama.

9. Ran girkinki, ba a qoshi da givi,
   Shi naman miyan ki canye a tsama.

10. In ta ga ka fito kamar za ka zaure,
    Sai sababi ya tashi don vata girma

11. Bar neman fita, ina tsame nama,
    Yau dai kai rabon, a zage ka kai ma.

12. Tun da ka sai kitse, ya narke a girki,
    In aka zo rabo, rabawansa fama.

13. Wanda ka ba shi qanqani, sai ya raina,

Kowa so shike ya karva da dama.

14. Rannan ma ka sai qashi na ci zagi,
Gun kwarin gidanka mai ya da girma.

15. In ta ce da ni *Qazama* in rama,
Wanda ya san Kumatu ya san *Qazama*.

16. In ta ce ina da ci ne in rama,
Domin ga Tasalla qoshnta fama.

17. Kwana goma jere, haifarta goma,
Ba taran miji ga haifar *Qazama*.

18. Ko bante ta qetare, sai ta haihu,
In ka san kuxi, su qare a suna.

19. Ya Allah daxa ma matanmu tsafta,
Kada Allah ka ba mu mata *Qazama*